# Suratun Naba'i

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

Tabbatar da afkuwar tashi bayan mutuwa, da ba da sakamako, da dalilai da hujjoji.

## Tafsir:

(1) Wane abu ne waxannan Mushirikai suke tambaya a kansa, bayan Allah ya aiko musu da Manzonsa (S.A.W)?! (2) Sashinsu yana tambayar sashi, a kan labari mai girma, shi ne wannan Alqur'anin da aka saukar ga Manzonsu, wanda ya qunshi labarin tashi bayan mutuwa. (3) Shi ne wannan Alqur'anin da suka yi savani a tsakaninsu, wurin siffata shi, shin tsafi ne, ko kuwa waqe ne, ko bokanci ne, ko tatsuniyoyin mutanen farko ne shi. (4) Lamarin ba kamar yadda suke riyawa ba ne, da sannu waxannan masu qaryatawa da Alqur'ani zasu san mummunan qarshen qaryatawar su. (5) Sannan da sannu hakan zai tabbata a gare su. (6) Shin bamu sanya qasa ta zama abar shimfixawa a gare su ba, ta yadda zasu iya rayuwa a bayanta?! (7) Kuma muka sanya duwatsu a kanta, suka zama kamar turaku ne da suke hana ta girgiza. (8) Kuma muka halicce ku - Ya ku mutane - iri daban daban, a cikinku akwai maza da mata. (9) Kuma muka sanya barcinku ya zama yankewa ne daga ayyukanku domin ku huta. (10) Kuma muka sanya dare ya zama mai suturce ku da duhunsa, kamar tufafin da kuke suturce al'aurar ku da shi. (11) Kuma muka sanya yini ya zama wani fili ne da ake neman arziki a cikinsa. (12) Kuma muka gina sammai guda bakwai a sama da ku, masu qwari, waxanda suke da kyan gini. (13) Kuma muka mayar da rana ta zama kamar fitila mai tsananin haskawa da kamawa. (14) Kuma muka saukar da ruwa mai yawan zuba daga girgijen da lokacin zubar da ruwansa ya yi. (15) Don mu fitar da qwaya kala-kala, da kala kalan tsirrai. (16) Kuma mu fitar da lambuna masu bishiyoyi luf-luf, saboda yadda reshensu yake shiga juna. Yayin da Allah ya ambaci waxannan ni'imomi da suke nuna ikonsa, sai ya biyo da maganar tashin alqiyama, domin wanda yake da ikon halittar waxannan ni'imomi, to mai iko ne a kan tayar da matattu da yi musu hisabi, sai ya ce: (17) Haqiqa ranar rarrabewa tsakanin halittu lokaci ne qayyadajje iyakantacce, ba zai sava ba. (18) Ranar da Mala'ika zai yi busa ta biyu a cikin qaho, sai ku mutane ku zo tawaga tawaga. (19) Kuma an buxe sama, ya zama tana da qofofi, kamar qofofin da aka buxe. (20) Kuma aka sanya duwatsu suna tafiya, har suka zama kamar tokar da aka sheqe, suka zama kamar kawalweniya. (21) Haqiqa wutar Jahannama ta kasance mai jira da yin dako. (22) Ga azzalumai, kuma makoma ce da zasu koma zuwa gare ta. (23) Za su zauna a cikinta lokuta da zamuna masu yawa, waxanda basu da iyaka. (24) Kuma ba zasu xanxani iska mai sanyi ba a cikinta, wadda za ta sanyaya musu zafin wutar da suke ciki, kuma ba zasu xanxani wani abin sha da zasu ji daxi da shi ba. (25) Basa xanxanar komai a cikinta sai wani ruwa mai tsananin zafi, da abin da yake kwaranyowa daga ruwan qurjin 'yan wuta. (26) Wannan sakamako ne wanda ya dace, da abin da suka kasance a kai na kafirci da savo. (27) Haqiqa su, sun kasance a duniya basa jin tsoron hisabin Allah a gare su a lahira, domin basu yin imani da tashi bayan mutuwa ba, don da ace suna jin tsoron tashi bayan mutuwa da sun yi imani da Allah, kuma da sun aikata ayyuka nagari. (28) Kuma sun qaryata ayoyinmu waxanda aka saukar wa Manzonmu dukkan qaryatawa. (29) Kuma komai na ayyukansu mun lissafe shi, kuma mun qididdige shi, kuma a rubuce yake a takardun ayyukansu. (30) Ya ku masu xagawa ku xanxani wannan azabar dauwamammiya, ba zamu qara muku komai ba sai azaba a kan azabar da kuke ciki.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Yadda Allah ya kyautata halitta yana nuna ikonsa na iya dawo da halittar bayan ta mutu. 2 - Yin xagawa yana kaiwa zuwa ga shiga wuta. 3 - Ninka azaba ga kafirai.



آياتها ٤٠ سُورَةُ النَّبَإِ ترتيبها ٧٨

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الجزء ٣٠ الحزب ٥٩
عَمَّ يَتَسَآءَلُونَ ١ عَنِ ٱلنَّبَإِ ٱلْعَظِيمِ ٢ ٱلَّذِى هُمْ فِيهِ مُخْتَلِفُونَ ٣
كَلَّا سَيَعْلَمُونَ ٤ ثُمَّ كَلَّا سَيَعْلَمُونَ ٥ أَلَمْ نَجْعَلِ ٱلْأَرْضَ مِهَٰدًا ٦
وَٱلْجِبَالَ أَوْتَادًا ٧ وَخَلَقْنَٰكُمْ أَزْوَٰجًا ٨ وَجَعَلْنَا نَوْمَكُمْ سُبَاتًا
٩ وَجَعَلْنَا ٱلَّيْلَ لِبَاسًا ١٠ وَجَعَلْنَا ٱلنَّهَارَ مَعَاشًا ١١ وَبَنَيْنَا
فَوْقَكُمْ سَبْعًا شِدَادًا ١٢ وَجَعَلْنَا سِرَاجًا وَهَّاجًا ١٣ وَأَنزَلْنَا مِنَ
ٱلْمُعْصِرَٰتِ مَآءً ثَجَّاجًا ١٤ لِّنُخْرِجَ بِهِۦ حَبًّا وَنَبَاتًا ١٥ وَجَنَّٰتٍ
أَلْفَافًا ١٦ إِنَّ يَوْمَ ٱلْفَصْلِ كَانَ مِيقَٰتًا ١٧ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ
فَتَأْتُونَ أَفْوَاجًا ١٨ وَفُتِحَتِ ٱلسَّمَآءُ فَكَانَتْ أَبْوَٰبًا ١٩ وَسُيِّرَتِ
ٱلْجِبَالُ فَكَانَتْ سَرَابًا ٢٠ إِنَّ جَهَنَّمَ كَانَتْ مِرْصَادًا ٢١ لِّلطَّٰغِينَ
مَـَٔابًا ٢٢ لَّٰبِثِينَ فِيهَآ أَحْقَابًا ٢٣ لَّا يَذُوقُونَ فِيهَا بَرْدًا وَلَا شَرَابًا
٢٤ إِلَّا حَمِيمًا وَغَسَّاقًا ٢٥ جَزَآءً وِفَاقًا ٢٦ إِنَّهُمْ كَانُوا۟
لَا يَرْجُونَ حِسَابًا ٢٧ وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا كِذَّابًا ٢٨ وَكُلَّ شَىْءٍ
أَحْصَيْنَٰهُ كِتَٰبًا ٢٩ فَذُوقُوا۟ فَلَن نَّزِيدَكُمْ إِلَّا عَذَابًا ٣٠

إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ مَفَازًا ٣١ حَدَآئِقَ وَأَعْنَٰبًا ٣٢ وَكَوَاعِبَ أَتْرَابًا ٣٣ وَكَأْسًا
دِهَاقًا ٣٤ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا وَلَا كِذَّٰبًا ٣٥ جَزَآءً مِّن رَّبِّكَ عَطَآءً
حِسَابًا ٣٦ رَّبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ٱلرَّحْمَٰنِ لَا يَمْلِكُونَ
مِنْهُ خِطَابًا ٣٧ يَوْمَ يَقُومُ ٱلرُّوحُ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ صَفًّا لَّا يَتَكَلَّمُونَ
إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَقَالَ صَوَابًا ٣٨ ذَٰلِكَ ٱلْيَوْمُ ٱلْحَقُّ فَمَن
شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ٣٩ إِنَّآ أَنذَرْنَٰكُمْ عَذَابًا قَرِيبًا يَوْمَ يَنظُرُ
ٱلْمَرْءُ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ وَيَقُولُ ٱلْكَافِرُ يَٰلَيْتَنِى كُنتُ تُرَٰبًۢا ٤٠

ترتيبها ٧٩ — سُورَةُ النَّازِعَاتِ — آياتها ٤٦

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلنَّٰزِعَٰتِ غَرْقًا ١ وَٱلنَّٰشِطَٰتِ نَشْطًا ٢ وَٱلسَّٰبِحَٰتِ سَبْحًا ٣
فَٱلسَّٰبِقَٰتِ سَبْقًا ٤ فَٱلْمُدَبِّرَٰتِ أَمْرًا ٥ يَوْمَ تَرْجُفُ ٱلرَّاجِفَةُ ٦
تَتْبَعُهَا ٱلرَّادِفَةُ ٧ قُلُوبٌ يَوْمَئِذٍ وَاجِفَةٌ ٨ أَبْصَٰرُهَا خَٰشِعَةٌ ٩
يَقُولُونَ أَءِنَّا لَمَرْدُودُونَ فِى ٱلْحَافِرَةِ ١٠ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمًا نَّخِرَةً ١١ قَالُوا۟
تِلْكَ إِذًا كَرَّةٌ خَاسِرَةٌ ١٢ فَإِنَّمَا هِىَ زَجْرَةٌ وَٰحِدَةٌ ١٣ فَإِذَا هُم بِٱلسَّاهِرَةِ
١٤ هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ١٥ إِذْ نَادَىٰهُ رَبُّهُۥ بِٱلْوَادِ ٱلْمُقَدَّسِ طُوًى ١٦



**(31) Haqiqa masu jin tsoron Ubangijinsu ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, suna da wuri, da zasu rabauta a cikinsa da abin da suke nema, shi ne Aljannah. (32) Gonaki da inabi kala-kala. (33) Da 'yan mata sa'annin juna. (34) Ga kofunan giya a cike da ita. (35) Kuma basa jin wata magana ta banza a cikin gidan Aljannah, basa jin qarya, kuma sashensu baya yi wa sashe qarya. (36) Duk wannan abubuwa suna daga cikin abin da Allah ya ba su, kyauta da baiwa isasshiya. (37) Ubangijin sammai da qassai kuma Ubangijin abin da yake tsakaninsu, kuma mai jin qan bayi a duniya da lahira, duk waxanda suke cikin sama da qasa basu da damar su tambaye shi, sai idan ya ba su izini. (38) A ranar da Mala'ika jibrilu da sauran Mala'iku zasu tsaya sahu-sahu, kuma baza su yi maganar ceton wani ba, sai wanda Allah mai rahama ya bada izinin a cece shi, kuma ya faxi magana ta daidai kamar kalmar shahada. (39) Wannan rana da aka siffanta muku ita ce ranar da babu makawa sai ta zo, to duk mai son ya kuvuta daga azabar Allah to ya kama hanyar da zata kuvutar da shi xin, ta hanyar ayyuka nagari, waxanda zasu janyo masa yardar ubangijinsa. (40) Ya ku mutane haqiqa mun tsoratar da ku azaba ta kurkusa da zata faru, a ranar da mutum zai kalli abin da ya gabatar na ayyuka a duniya, kuma kafiri zai yi burin kuvuta daga azaba ya ce: "Ina ma dai na zama qasa kamar sauran dabbobi". Lokacin da za a ce musu: "Duk ku zama turvaya".**

# Suratun Nazi'at

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Qwanqwasar zukatan da suke qaryata tashin alqiyama da bada sakamako, ta hanyar bijiro da abubuwan mutuwa, da tashin alqiyama, da tara mutane, da bayanin sauran al'amuran alqiyama.**

**Tafsir:** **(1) Allah ya rantse da Mala'ikun da suke fizgar rayukan kafirai cikin tsanani da rashin tausayawa. (2) Kuma ya rantse da Mala'ikun da suke zare ran Muminai cikin sauqi da sassautawa. (3) Kuma ya rantse da Mala'ikun da suke linqaya daga sama zuwa qasa da umarnin Allah. (4) Kuma ya rantse da Mala'iku waxanda suke rigeggeniya da junansu wurin gabatar da umarnin Allah. (5) Kuma ya rantse da Mala'iku masu zartar da abin da Allah ya umarce su na daga hukunce-hukuncensa, kamar Mala'ikun da aka wakilta a kan ayyukan bayi. Allah ya rantse da waxannan duka akan cewa tabbas zai tashi bayi don yi musu hisabi da bada sakamako. (6) A ranar da qasa zata yi girgiza yayin busa ta farko. (7) Kuma busa ta biyu tana biye da ta farkon. (8) Zukatan wasu mutane a wannan rana cike suke da tsoro. (9) Kuma alamun qasqanci suna bayyana a idanunsu. (10) Kuma sun kasance suna cewa: "Shin zamu komo ga rayuwa bayan mun mutu?!". (11) Yanzu bayan mun zamo rididdigaggun qasusuwa fanko, a ce zamu dawo wata rayuwar bayan haka? (12) Sai suka ce: "Idan har da gaske ne zamu dawo to wannan dawowar akwai asara a cikinta, kuma ma'abocinta zai yi fargar jaji". (13) Lamarin dawowa bayan mutuwa mai sauqi ne, maganace ta busa guda xaya kawai daga Mala'ikan da aka wakilta ya yi busa. (14) Sai ga kowa ya dawo a raye a bayan qasa, bayan duk sun kasance matattu a cikin qasa. (15) Shin labarin Annabi Musa tare da Ubangijinsu da kuma maqiyinsa Fir'auna yazo maka, ya kai wannan Manzo?! (16) Lokacin da Ubangijin shi ya kira shi, a wani kwari da ake kira (Xuwa) mai tsarki.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Tsoron Allah ne sababin shiga gidan Aljannah. 2 - Tunawa da tashin hankalin ranar alqiyama yana qara sa himma wajen aiki nagari. 3 - Karvar ran kafiri ana yin sa ne cikin tsanani da wahala, kuma ana karvar ran mumini cikin tausasawa da lausasawa.**

ٱذۡهَبۡ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ١٧ فَقُلۡ هَل لَّكَ إِلَىٰٓ أَن تَزَكَّىٰ ١٨ وَأَهۡدِيَكَ
إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخۡشَىٰ ١٩ فَأَرَىٰهُ ٱلۡأٓيَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٢٠ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ٢١ ثُمَّ
أَدۡبَرَ يَسۡعَىٰ ٢٢ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ٢٣ فَقَالَ أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٤ فَأَخَذَهُ
ٱللَّهُ نَكَالَ ٱلۡأٓخِرَةِ وَٱلۡأُولَىٰٓ ٢٥ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ ٢٦
ءَأَنتُمۡ أَشَدُّ خَلۡقًا أَمِ ٱلسَّمَآءُۚ بَنَىٰهَا ٢٧ رَفَعَ سَمۡكَهَا فَسَوَّىٰهَا ٢٨
وَأَغۡطَشَ لَيۡلَهَا وَأَخۡرَجَ ضُحَىٰهَا ٢٩ وَٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ دَحَىٰهَآ ٣٠
أَخۡرَجَ مِنۡهَا مَآءَهَا وَمَرۡعَىٰهَا ٣١ وَٱلۡجِبَالَ أَرۡسَىٰهَا ٣٢ مَتَٰعٗا لَّكُمۡ
وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٣ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلطَّآمَّةُ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٣٤ يَوۡمَ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ
مَا سَعَىٰ ٣٥ وَبُرِّزَتِ ٱلۡجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ٣٦ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ٣٧ وَءَاثَرَ
ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ٣٨ فَإِنَّ ٱلۡجَحِيمَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ٣٩ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ
مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ٤٠ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ
٤١ يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرۡسَىٰهَا ٤٢ فِيمَ أَنتَ مِن
ذِكۡرَىٰهَآ ٤٣ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَىٰهَآ ٤٤ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخۡشَىٰهَا
٤٥ كَأَنَّهُمۡ يَوۡمَ يَرَوۡنَهَا لَمۡ يَلۡبَثُوٓاْ إِلَّا عَشِيَّةً أَوۡ ضُحَىٰهَا ٤٦

آياتها ٤٢ — سُورَةُ عَبَسَ — ترتيبها ٨٠



**17** Daga cikin abin da ya faxa masa shi ne: "Ka tafi wurin Fir'auna, haqiqa ya qetare iyaka wajen zalunci da girman kai. **18** Ka ce masa: "Ya kai Fir'auna, shin zaka yarda ka tsarkaka daga aikata kafirci da savon Allah?" **19** Kuma in nusar da kai ga Ubangijinka wanda ya halicce ka, kuma ya kula da kai, don ka ji tsoronsa, kai aiki da abin da yake so, kuma ka nisanci abin da baya so?. **20** Sai Annabi Musa (A.S) ya nuna masa babbar hujja, wadda take nuna shi Manzo ne daga Ubangijinsa, ita ce hannunsa da sandarsa. **21** Fir'auna bai yi wani abu ba, sai kawai ya qaryata wannan alama da Annabi Musa ya nuna masa, ya savawa abin da Annabi Musa (A.S) ya umarce shi da shi. **22** Sannan ya bijirewa imani da abin da Annabi Musa ya zo da shi. **23** Ya koma yana tara rundunarsa, domin ya samu galaba a kan Annabi Musa, ya kira mutanensa ya ce:
**24** Ni ne Ubangijinku mafi girma, don haka babu biyayya ga wani a kanku wanda ba ni ba. **25** Sai Allah ya kama shi, ya yi masa uquba a nan duniya ta hanyar nutsarwa a teku, kuma ya yi masa uquba a lahira ta hanyar shigar da shi mafi tsananin azaba. **26** Haqiqa a cikin uqubar da muka yi wa Fir'auna a duniya da lahira akwai wa'azi ga mai tsoron Allah, domin shi ne yake amfana da wa'azi. **27** Shin samar da ku - Ya ku masu qaryatawa da tashin alqiyama – shi ne yafi wahala, ko kuwa samar da sama wadda Allah ya gina ta? **28** Kuma ya sanya siffarta ta wajen sama maxaukakiya, ya sanya ta daidaitacciya, babu tsagewa, ko aibu ko wani abu a jikinta.
**29** Kuma ya sanya daren ta mai duhu idan ranar ta ta faxi, sannan ya bayyana haskenta idan ranar ta fito.
**30** Qasa kuma bayan ya halicci sama sai ya shimfixa ta, ya sanya kayan amfaninta a cikinta.
**31** Ya fitar da ruwan da yake cikin qasar, ya sanya su idanuwa suna gudana, ya fitar da tsirrai daga cikinta, wanda dabbobi suke kiwo da shi. **32** Duwatsu kuma ya sanya su tabbatattu a bayan qasa.
**33** Duk wannan domin amfanin ku – Ya ku mutane - da na dabbobin ku. To wanda ya halicci waxannan abubuwa duka ai ba zai kasa dawo da halittarsu ba a karo na biyu. **34** To idan busa ta biyu ta zo, wadda take mamaye komai da razanarwarta, kuma alqiyama ta tsaya. **35** Ranar da zata zo mutum zai tuna duk abin da ya gabatar na aiki, alheri ne ko sharri. **36** Kuma aka zo da wutar Jahannama, aka bayyanata a fili ga duk mai ganinta.
**37** Amma duk wanda ya qetare iyaka a vata. **38** Kuma ya fifita rayuwar duniya mai qarewa a kan rayuwar lahira mai dauwama. **39** To haqiqa wuta ita ce matabbatarsa da zai koma gare ta.
**40** **41** Amma wanda duk ya ji tsoron tsayuwa a gaban Ubangijinsa, kuma ya tsare kansa daga biyewa son zuciyarsa cikin abubuwan da Allah ya haramta, to tabbas Aljannah ce matabbatarsa da zai koma gare ta.
**42** Ya kai wannan Manzo waxannan masu qaryatawa da tashin alqiyama suna tambayarka cewa: "Yaushe ne alqiyama zata tashi?. **43** Baka da wani ilimi a kan lokacinta ballantana ka faxa musu, kuma yin haka ba aikin ka ba ne, aikinka kawai ka yi shiri domin wannan rana. **44** Zuwa ga Ubangijinka kaxai sanin lokacin alqiyama ya tuqe. **45** Haqiqa kai ba wani ba ne face mai gargaxi ga wanda yake tsoron tashin alqiyamar, don shi ne kaxai zai amfanu da gargaxin ka.
**46** Kai kace su a lokacin da zasu ga tashin alqiyamar, basu zauna wani lokaci a duniya ba, sai wani yammaci na yini xaya, ko kuma safiyar yini xaya.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Wajabcin tausasawa yayin da ake magana da wanda ake kira zuwa ga Allah. 2 - Tsoron Allah da hana rai son zuciyarta, yana daga cikin sabuban shiga Aljannah. 3 - Sanin lokacin tashin alqiyama yana cikin gaibun da babu wanda ya san shi sai Allah.
4 - Bayani dalla dalla da Allah ya yi na halittar sama da qasa.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

عَبَسَ وَتَوَلَّىٰٓ ١ أَن جَآءَهُ ٱلۡأَعۡمَىٰ ٢ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّهُۥ يَزَّكَّىٰٓ ٣ ربع الحزب ٥٩
أَوۡ يَذَّكَّرُ فَتَنفَعَهُ ٱلذِّكۡرَىٰٓ ٤ أَمَّا مَنِ ٱسۡتَغۡنَىٰ ٥ فَأَنتَ لَهُۥ تَصَدَّىٰ
٦ وَمَا عَلَيۡكَ أَلَّا يَزَّكَّىٰ ٧ وَأَمَّا مَن جَآءَكَ يَسۡعَىٰ ٨ وَهُوَ يَخۡشَىٰ ٩
فَأَنتَ عَنۡهُ تَلَهَّىٰ ١٠ كَلَّآ إِنَّهَا تَذۡكِرَةٞ ١١ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ١٢ فِي صُحُفٖ
مُّكَرَّمَةٖ ١٣ مَّرۡفُوعَةٖ مُّطَهَّرَةِۭ ١٤ بِأَيۡدِي سَفَرَةٖ ١٥ كِرَامِۭ بَرَرَةٖ ١٦
قُتِلَ ٱلۡإِنسَٰنُ مَآ أَكۡفَرَهُۥ ١٧ مِنۡ أَيِّ شَيۡءٍ خَلَقَهُۥ ١٨ مِن نُّطۡفَةٍ
خَلَقَهُۥ فَقَدَّرَهُۥ ١٩ ثُمَّ ٱلسَّبِيلَ يَسَّرَهُۥ ٢٠ ثُمَّ أَمَاتَهُۥ فَأَقۡبَرَهُۥ ٢١ ثُمَّ إِذَا
شَآءَ أَنشَرَهُۥ ٢٢ كَلَّا لَمَّا يَقۡضِ مَآ أَمَرَهُۥ ٢٣ فَلۡيَنظُرِ ٱلۡإِنسَٰنُ إِلَىٰ طَعَامِهِۦٓ
٢٤ أَنَّا صَبَبۡنَا ٱلۡمَآءَ صَبّٗا ٢٥ ثُمَّ شَقَقۡنَا ٱلۡأَرۡضَ شَقّٗا ٢٦ فَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا
حَبّٗا ٢٧ وَعِنَبٗا وَقَضۡبٗا ٢٨ وَزَيۡتُونٗا وَنَخۡلٗا ٢٩ وَحَدَآئِقَ غُلۡبٗا ٣٠ وَفَٰكِهَةٗ
وَأَبّٗا ٣١ مَّتَٰعٗا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٢ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلصَّآخَّةُ ٣٣ يَوۡمَ يَفِرُّ
ٱلۡمَرۡءُ مِنۡ أَخِيهِ ٣٤ وَأُمِّهِۦ وَأَبِيهِ ٣٥ وَصَٰحِبَتِهِۦ وَبَنِيهِ ٣٦ لِكُلِّ
ٱمۡرِيٕٖ مِّنۡهُمۡ يَوۡمَئِذٖ شَأۡنٞ يُغۡنِيهِ ٣٧ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ مُّسۡفِرَةٞ
٣٨ ضَاحِكَةٞ مُّسۡتَبۡشِرَةٞ ٣٩ وَوُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ عَلَيۡهَا غَبَرَةٞ ٤٠



# Suratu Abasa

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin haqiqanin da'awar Alqur'ani, da girmar wanda yake amfanuwa da da'awar, da wulaqantar wanda bijire mata.**

## Tafsir:

**(1) Annabi (S.A.W) ya xaure fuskarsa, kuma ya bada baya. (2) Saboda zuwan Abdullahi xan ummu Maktum yana neman shiriya daga wurinsa, kuma ya kasance makaho ne, ya zo lokacin da Annabi ya shagaltu da manya manyan Mushirikai, yana mai tsammanin shiriyarsu.**
**(3) Me ya sanar da kai - Ya kai wannan Manzo - ko wannan makaho zai tsarkaka daga zunubansa?!**
**(4) Ko kuma ya wa'azantu da abin da yake wurinka na wa'azi, kuma ya amfana da shi.**
**(5) Amma ka ga wanda ya wadatu da kansa, ya qi yin imani, saboda abin da yake da shi na dukiya.**
**(6) Kai kuma kana qoqarin isar masa da saqo, kuma kana mayar da hankali a kansa.**
**(7) To me zai same ka idan bai tsarkaka daga zunubansa ba, ta hanyar tuba zuwa ga Allah?**
**(8) Amma wanda ya zo maka yana gaggawa, yana mai neman alheri.**
**(9) Kuma yana jin tsoron Ubangijinsa.**
**(10) Amma kai kuma kana shagalta daga barinsa, ka shagala da wasu cikin manyan Mushirikai.**
**(11) Lamarin ba haka yake ba, haqiqa wa'azi ne da tunatarwa ga wanda zai karva.**
**(12) Kuma duk wanda ya so ya tuna Allah sai ya tuna shi, ya wa'azantu da abin da yake cikin Alqur'ani. (13) Wannan Alqur'anin yana cikin takardu masu daraja a wurin Mala'iku. (14) Kuma maxaukaka a wuri mai xaukaka, kuma masu tsarki, babu wani datti ko qazanta da take samun su. (15) Suna hannun Manzanni daga cikin Mala'iku. (16) Masu girma a wurin Ubangijinsu, masu yawan aikata alheri da xa'a. (17) An tsinewa mutum kafiri, mamakin tsananin kafircinsa ga Allah! (18) Daga me Allah ya halicce shi, da har zai yi girman kai a bayan qasa, kuma ya kafirce masa?!. (19) Daga xan qanqanin ruwa ya halicce shi, kuma ya tsara halittarsa mataki bayan mataki. (20) Sannan ya sauwaqe masa fitowa daga cikin mahaifiyarsa bayan waxancan matakai na halitta. (21) Sannan kuma bayan ya gama abin da ya qaddara masa na shekarun da zai yi a duniya, sai ya kashe shi, ya sanya masa qabari, har zuwa lokacin da za a tashe shi. (22) Sannan idan ya ga dama ya tashe shi domin yi masa hisabi da sakayya. (23) Lamarin ba kamar yadda wannan kafiri yake tunani ba ne, cewa ya gama sauke nauyin Ubangijinsa da yake kansa, domin bai sauke abin da Allah ya wajabta masa na farilla ba. (24) Mutum kafiri ya yi duba mana zuwa ga abincinsa da yake ci, ta yaya ya same shi?! (25) Asalinsa daga ruwan sama ne, wanda yake sauka daga sama da qarfi da yawan gaske. (26) Sannan muka keta qasa, sai ta tsage tsirrai suka fito. (27) Sai muka fitar da qwayoyi na alkama da masara da sauransu daga cikinta. (28) Muka fitar da inibi da ciyawa, don ta zama abincin dabbobinsu. (29) Muka fitar da zaitun da dabino daga cikinta. (30) Kuma muka fitar da lambuna masu yawan bishiyoyi a cikinta. (31) Muka fitar da kayan marmari a cikinta, kuma muka fitar da abin da dabbobin ku zasu yi kiwo, su ci. (32) Duk wannan domin amfaninku ne, da kuma amfanin dabbobin ku. (33) Idan babbar tsawa ta zo, wadda take cika kunne, wato busa ta biyu kenan. (34) Ranar da mutum yake gujewa xan uwansa. (35) Ya gujewa mahaifiyarsa da mahaifinsa. (36) Ya gujewa matarsa da 'ya'yansa. (37) Kowane daga cikinsu a ranar yana da abin da ya shagaltar da shi daga xan uwansa, na tsananin damuwa a wannan rana. (38) Fuskokin 'yan Aljannah a wannan ranar walqiya suke yi. (39) Suna cikin dariya da farin cikin abin da Allah ya tanadar musu na jin qansa. (40) Fuskokin 'yan wuta a wannan ranar sun yi qura babu kyan gani.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Zargin Allah ga Manzonsa akan lamarin Abdullah xan Ummu Maktum, yana nuna cewa Alqur'ani daga wurin Allah yake. 2 - Kula da mai neman ilimi da mai neman shiriya. 3 - Tsananin da yake cikin tashin alqiyama, ta yadda kowa ta kansa yake yi, har Annabawa cewa suke yi: ta kaina nake yi, ta kaina nake yi.**

تَرْهَقُهَا قَتَرَةٌ ﴿٤١﴾ أُولَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَفَرَةُ ٱلْفَجَرَةُ ﴿٤٢﴾

آياتها ٢٩ — سُورَةُ التَّكْوِيرِ — ترتيبها ٨١

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا ٱلشَّمْسُ كُوِّرَتْ ﴿١﴾ وَإِذَا ٱلنُّجُومُ ٱنكَدَرَتْ ﴿٢﴾ وَإِذَا ٱلْجِبَالُ
سُيِّرَتْ ﴿٣﴾ وَإِذَا ٱلْعِشَارُ عُطِّلَتْ ﴿٤﴾ وَإِذَا ٱلْوُحُوشُ حُشِرَتْ
﴿٥﴾ وَإِذَا ٱلْبِحَارُ سُجِّرَتْ ﴿٦﴾ وَإِذَا ٱلنُّفُوسُ زُوِّجَتْ ﴿٧﴾ وَإِذَا
ٱلْمَوْءُۥدَةُ سُئِلَتْ ﴿٨﴾ بِأَيِّ ذَنۢبٍ قُتِلَتْ ﴿٩﴾ وَإِذَا ٱلصُّحُفُ نُشِرَتْ
﴿١٠﴾ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ كُشِطَتْ ﴿١١﴾ وَإِذَا ٱلْجَحِيمُ سُعِّرَتْ ﴿١٢﴾ وَإِذَا ٱلْجَنَّةُ
أُزْلِفَتْ ﴿١٣﴾ عَلِمَتْ نَفْسٌ مَّآ أَحْضَرَتْ ﴿١٤﴾ فَلَآ أُقْسِمُ بِٱلْخُنَّسِ ﴿١٥﴾
ٱلْجَوَارِ ٱلْكُنَّسِ ﴿١٦﴾ وَٱلَّيْلِ إِذَا عَسْعَسَ ﴿١٧﴾ وَٱلصُّبْحِ إِذَا تَنَفَّسَ ﴿١٨﴾
إِنَّهُۥ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ﴿١٩﴾ ذِى قُوَّةٍ عِندَ ذِى ٱلْعَرْشِ مَكِينٍ ﴿٢٠﴾ مُّطَاعٍ
ثَمَّ أَمِينٍ ﴿٢١﴾ وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجْنُونٍ ﴿٢٢﴾ وَلَقَدْ رَءَاهُ بِٱلْأُفُقِ ٱلْمُبِينِ
﴿٢٣﴾ وَمَا هُوَ عَلَى ٱلْغَيْبِ بِضَنِينٍ ﴿٢٤﴾ وَمَا هُوَ بِقَوْلِ شَيْطَٰنٍ رَّجِيمٍ ﴿٢٥﴾
فَأَيْنَ تَذْهَبُونَ ﴿٢٦﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٧﴾ لِمَن شَآءَ مِنكُمْ أَن
يَسْتَقِيمَ ﴿٢٨﴾ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٩﴾



**(41) Duhu ya baibaye ta. (42) Waxannan da aka siffanta da wancan hali su ne waxanda suka haxa tsakanin kafirci da fajirci.**

## Suratut Takwir

An Saukar Da Ita A Makkah

### Daga Manufofin Surar:

**Suranta tashin alqiyama, ta hanyar rikicewar duniya bayan da tana tafiya a tsare.**

### Tafsir:

**(1) Idan rana aka tattara jikinta, kuma haskenta ya tafi. (2) Idan taurari suka faxo, kuma aka shafe haskensu.**
**(3) Idan aka motsa duwatsu daga wurinsu.**
**(4) Idan taguwoyi masu ciki - waxanda su ne mafi tsadar dukiyoyinsu - aka watsar da su, waxanda suka mallake su suka yi bar su. (5) Idan aka tara dabbobin daji da mutane a fili guda.**
**(6) Idan tekuna aka kunna su, har suka zama wuta suna ci. (7) Idan aka haxa kowane rayuka da waxanda suka dace da su, aka haxa fajiri da fajiri, mai tsoron Allah da mai tsoron Allah.**
**(8) Idan yarinyar da aka binne ta da ran ta Allah ya tambaye ta. (9) Da wane laifi ne wanda ya kashe ki ya kashe ki?! (10) Idan aka yaxa takardun ayyukan bayi, domin kowa ya karanta takardar aikinsa. (11) Idan sama aka kwayeta, kamar yadda ake kwaye fata daga jikin tinkiya.**
**(12) Idan aka rura wuta. (13) Idan aka gabato da Aljannah ga masu tsoron Allah. (14) A yayin da haka zai wakana, kowace rai zata san abin da ta gabatar na ayyuka, domin wannan rana.**
**(15) Allah ya rantse da taurari masu vuya kafin su fito da daddare.**
**(16) Masu gudu a cikin falakinsu, waxanda suke vuya yayin fitowa asubahi, suna gudu kamar barewa tana shiga gidanta. (17) Kuma ya rantse da farkon dare yayin da ya fuskanto, da kuma qarshensa yayin da ya bada baya.**
**(18) Kuma ya rantse da asubahi yayin da haskensa ya bayyana.**
**(19) Haqiqa Alqur'anin da aka saukar wa Muhammad (S.A.W) tabbas maganar Allah ce, da amintaccen Mala'ika ya isar masa da shi, shi ne Mala'ika jibrilu (A.S) wanda Allah ya amince masa a kan Alqur'ani.**
**(20) Ma'abocin qarfi, mai babban matsayi a wajen Ubangijin al'arshi mai girma.**
**(21) Waxanda suke cikin sama suna yi masa biyayya, kuma amintacce a cikin abin da yake isarwa na wahayi.**
**(22) Kuma Muhammad (S.A.W) wanda kullum yana tare da ku, kuma kun san hankalinsa, da amanarsa, da gaskiyarsa, ba mahaukaci ba ne, kamar yadda kuke riyawa, saboda tsabar qarya.**
**(23) Tabbas xan uwanku ya ga Mala'ika jibrilu a haqiqanin halittarsa da aka halicce shi a kanta a sasannin sama.**
**(24) Kuma xan uwanku ba marowaci ba ne, ballantana ya yi muku rowar isar da abin da aka umarce shi da isarwa gare ku, kuma baya karvar lada kamar yadda bokaye suke karva.**
**(25) Wannan Alqur'ani ba maganar shaixan abin kora daga rahamar Allah ba ne.**
**(26) To wace hanya kuke bi domin yin inkarin cewa shi Alqur'ani ba daga Allah yake ba, bayan waxannan dalilai kuma?!. (27) Alqur'ani ba komai ba ne face tunatarwa da wa'azi ga aljanu da mutane.**
**(28) Ga wanda ya so daga cikinku ya tsaya a kan tafarki madaidaici. (29) Sai dai ba zaku so tsayawa a kan tafarki madaidaici ba, ko wani abu, face sai idan Allah ya so hakan, Ubangijin halitta gaba xaya.**

### Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Za a tashi mutum a haxa shi da makamantansa a cikin alheri ko kuma sharri.**
**2 - Idan har yarinyar da aka binne ta da ranta za a tambayeta, to ina ga kuma ga wanda ya binneta?!. Kuma wannan yana nuna girman wannan lokaci.**
**3 - Abin da bawa yake so, yana bin bayan abin da Allah yake so ne.**

سُورَةُ الانفِطَارِ
آياتها ١٩ — ترتيبها ٨٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

نصف الحزب ٥٩ إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنفَطَرَتۡ ١ وَإِذَا ٱلۡكَوَاكِبُ ٱنتَثَرَتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ
فُجِّرَتۡ ٣ وَإِذَا ٱلۡقُبُورُ بُعۡثِرَتۡ ٤ عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ
وَأَخَّرَتۡ ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ ٱلۡكَرِيمِ ٦ ٱلَّذِي
خَلَقَكَ فَسَوَّىٰكَ فَعَدَلَكَ ٧ فِيٓ أَيِّ صُورَةٖ مَّا شَآءَ رَكَّبَكَ ٨
كَلَّا بَلۡ تُكَذِّبُونَ بِٱلدِّينِ ٩ وَإِنَّ عَلَيۡكُمۡ لَحَٰفِظِينَ ١٠ كِرَامٗا
كَٰتِبِينَ ١١ يَعۡلَمُونَ مَا تَفۡعَلُونَ ١٢ إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٖ ١٣ وَإِنَّ
ٱلۡفُجَّارَ لَفِي جَحِيمٖ ١٤ يَصۡلَوۡنَهَا يَوۡمَ ٱلدِّينِ ١٥ وَمَا هُمۡ عَنۡهَا بِغَآئِبِينَ
١٦ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ١٧ ثُمَّ مَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ
١٨ يَوۡمَ لَا تَمۡلِكُ نَفۡسٞ لِّنَفۡسٖ شَيۡـٔٗاۖ وَٱلۡأَمۡرُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ ١٩

سُورَةُ المُطَفِّفِينَ
آياتها ٣٦ — ترتيبها ٨٣

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَيۡلٞ لِّلۡمُطَفِّفِينَ ١ ٱلَّذِينَ إِذَا ٱكۡتَالُواْ عَلَى ٱلنَّاسِ يَسۡتَوۡفُونَ ٢
وَإِذَا كَالُوهُمۡ أَو وَّزَنُوهُمۡ يُخۡسِرُونَ ٣ أَلَا يَظُنُّ أُوْلَٰٓئِكَ أَنَّهُم مَّبۡعُوثُونَ ٤



# Suratul linfixar

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Suranta yadda alqiyama zata wakana, ta hanyar watsewar halittu, da canjin hali da yanayin da suke kai, waxanda a da suke cikin tsari.**

## Tafsir:

**(1) Idan sama ta kekkece, domin saukar Mala'iku daga cikinta.**
**(2) Kuma idan taurari suka faxo a tarwatse.**
**(3) Kuma idan teku aka buxe su, duk suka haxe da juna. (4) Kuma idan qaburbura aka juya qasarsu, domin tayar da waxanda suke cikinsu daga mamata. (5) A wannan lokaci kowace rai zata san abin da ta gabatar na ayyuka, da kuma abin da ta jinkirta bata aikata ba. (6) Ya kai wannan mutum mai kafirce wa Ubangijinka, mene ne ya sa kake savawa umarnin Ubangijinka, yayin da ya jinkirta maka, bai gaggauta maka azabarsa ba, saboda girmamawa daga gare shi?!.**
**(7) Wanda ya samar da kai bayan ka kasance babu, kuma ya sanya ka mai daidaitun gavvai masu kyau. (8) Kuma a kowace sura ya ga damar halittarka sai ya halicce ka, kuma haqiqa ya yi maka ni'ima da bai halicce ka a surar jaki ba, ko biri, ko kare ko makamantansu.**
**(9) Lamarin ba kamar yadda kuke tunani ba ne - Ya ku masu ruxuwa - kawai dai kuna qaryatawa ne da ranar sakamako, don haka ba kwa yin aiki don wannan ranar.**
**(10) Kuma tabbas akwai mala'iku tare da ku masu kiyaye ayyukanku.**
**(11) Masu girma a wurin Allah, kuma marubuta, suna rubuta ayyukanku. (12) Sun san abin da kuke aikatawa na kowane aiki, kuma suna rubuta shi. (13) Haqiqa masu yawaita ayyukan alheri da xa'a suna cikin madauwamiyar ni'ima ranar alqiyama. (14) Kuma tabbas ma'abota fajirci suna cikin wuta, wadda ake daxa ruruta a kansu.**
**(15) Zasu shige ta a ranar sakamako, kuma su sha fama da zafinta. (16) Kuma ba zasu fita daga cikinta ba har abada, zasu dauwama a cikinta ne. (17) Ya kai wannan Manzo, me ya sanar da kai ranar sakamako?! (18) Sannan kuma me ya sanar da kai ranar sakamako?! (19) Ranar da wani bai isa ya amfanawa wani komai ba, kuma dukkan lamari na Allah ne shi kaxai a wannan rana, yana yin yadda ya ga dama, ba wani wanda yake da wannan rana wanda ba shi ba.**

# Suratul Muxaffifeen

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Suran ta maida hankali ne a kan bayanin halin mutane, yayin auna ayyukansu, da kuma gidajensu na lahira, domin tsoratar da masu tauye ma'auni da maqaryata, da kuma rarrashin Muminai masu rauni.**

## Tafsir:

**(1) Halaka da asara sun tabbata ga masu tauye ma'auni.**
**(2) Su ne waxanda idan zasu yi awo daga waninsu, sai su nemi a cika musu haqqinsu, ba tare da ragi ba.**
**(3) Amma idan su ne zasu aunawa mutane, ko kuma su gwada musu, sai su tauye ma'auni ko magwajin. Haka halin mutanen Madinah yake, lokacin da Annabi (S.A.W) ya yi hijira zuwa gare su. (4) Yanzu waxannan masu aikata wannan mummunan aiki basu sakankance da cewa za a tashe su a gaban Allah ba?!.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsoratarwa a kan ruxuwar da take hana bin gaskiya. 2 - Handama da babakere suna cikin munanan halayen 'yan kasuwa, babu wanda yake kuvuta daga gare su sai wanda yake jin tsoron Allah. 3 - Tunawa da tashin hankalin ranar alqiyama yana daga cikin manya-manyan abubuwa da suke tsawatar wa ga barin savo.**

لِيَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥ يَوۡمَ يَقُومُ ٱلنَّاسُ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ
ٱلۡفُجَّارِ لَفِي سِجِّينٖ ٧ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا سِجِّينٞ ٨ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ٩
وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٠ ٱلَّذِينَ يُكَذِّبُونَ بِيَوۡمِ ٱلدِّينِ ١١ وَمَا يُكَذِّبُ
بِهِۦٓ إِلَّا كُلُّ مُعۡتَدٍ أَثِيمٍ ١٢ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ
١٣ كَلَّاۖ بَلۡۜ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ١٤ كَلَّآ إِنَّهُمۡ عَن رَّبِّهِمۡ
يَوۡمَئِذٖ لَّمَحۡجُوبُونَ ١٥ ثُمَّ إِنَّهُمۡ لَصَالُواْ ٱلۡجَحِيمِ ١٦ ثُمَّ يُقَالُ هَٰذَا
ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ١٧ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلۡأَبۡرَارِ لَفِي عِلِّيِّينَ ١٨
وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا عِلِّيُّونَ ١٩ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ٢٠ يَشۡهَدُهُ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢١
إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٍ ٢٢ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٢٣ تَعۡرِفُ فِي
وُجُوهِهِمۡ نَضۡرَةَ ٱلنَّعِيمِ ٢٤ يُسۡقَوۡنَ مِن رَّحِيقٖ مَّخۡتُومٍ ٢٥ خِتَٰمُهُۥ
مِسۡكٞۚ وَفِي ذَٰلِكَ فَلۡيَتَنَافَسِ ٱلۡمُتَنَٰفِسُونَ ٢٦ وَمِزَاجُهُۥ مِن
تَسۡنِيمٍ ٢٧ عَيۡنٗا يَشۡرَبُ بِهَا ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ أَجۡرَمُواْ كَانُواْ
مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَضۡحَكُونَ ٢٩ وَإِذَا مَرُّواْ بِهِمۡ يَتَغَامَزُونَ ٣٠
وَإِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمُ ٱنقَلَبُواْ فَكِهِينَ ٣١ وَإِذَا رَأَوۡهُمۡ قَالُوٓاْ
إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ ٣٢ وَمَآ أُرۡسِلُواْ عَلَيۡهِمۡ حَٰفِظِينَ ٣٣

سكتة لطيفة على اللام



**(5) Domin yi hisabi da sakayya a rana mai girma, saboda abin da yake cikin wannan ranar na masifu da ban-tsoro. (6) Ranar da mutane zasu tsaya a gaban Ubangijin halittu gaba xaya domin yin hisabi. (7) Lamarin ba kamar yadda kuka surantawa ba ne, cewa babu tashi bayan mutuwa, kuma tabbas littafin ma'abota fajirci daga cikin kafirai da munafukai yana cikin Sijjinu a can qasa. (8) Menene ya sanar da kai Sijjinu ya kai wannan Manzo?! (9) Tabbas haqiqa littafinsu an gama rubuta shi, kuma ba zai goge ba, kuma ba za a qara wani abu ba, ba kuma za a rage ba.**

**(10) Halaka da asara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryatawa. (11) Su ne waxanda suke qaryatawa da ranar sakamako, ranar da Allah zai sakawa bayinsa bisa ayyukan da suka gabatar a duniya. (12) Babu wanda yake qaryata wannan rana sai mai qetare iyakokin Allah, kuma mai yawan savonsa. (13) Idan ana karanta masa ayoyinmu da aka saukarwa Manzonmu sai ya ce: "Wannan labaran mutanen farko ne, ba daga Allah suke ba". (14) Lamarin ba kamar yadda waxannan masu qaryatawa suke surantawa ba ne, kawai dai abubuwan da suke aikatawa na savon Allah su ne suka mamaye musu hankulansu, kuma suka rufe musu shi ruf, shi ne yasa basa iya ganin gaskiya da zukatansu. (15) Tabbas su dangane da ganin Ubangijinsu a ranar alqiyama ababen katangewa ne. (16) Sannan su haqiqa sai sun shiga wuta, su sha fama da zafinta.**

**(17) Sannan za a ce musu ranar alqiyama an tsorata su: "Wannan azabar da kuka gamu da ita, ita ce wadda kuka kasance kuna qaryatawa da ita a duniya, lokacin da Manzonku yake ba ku labarinta.**

**(18) Lamarin ba kamar yadda kuke surantawa ba ne, cewa babu wani hisabi kuma babu wata sakayya, tabbas littafin ma'abota xa'ar Allah yana cikin illiyina. (19) Me ya sanar da kai abin da ake nufi da illiyyina?!**

**(20) Tabbas littafi ne rubutacce, ba zai gushe ba, kuma baza a qara komai a cikinsa ba, kuma ba za a rage ba.**

**(21) Mala'iku makusanta a kowace sama suna halartar inda wannan littafi yake.**

**(22) Haqiqa masu yawaita xa'ar Allah suna cikin ni'ima dauwamammiya a ranar alqiyama.**

**(23) Akan gadaje masu ado, suna kallon Ubangijinsu, kuma suna kallon duk abin da zai faranta musu zukatansu ya sa su farin ciki. (24) Kuma idan ka gan su to tabbas zaka ga alamun ni'ima a fuskokinsu da kwarjini.**

**(25) Masu yi musu hidima suna shayar da su daga wata giya wadda aka rufe bakinta?.**

**(26) Qanshin almiski yana tashi daga wannan giyar har zuwa qarshen ta. A cikin irin wannan sakamako mai girma ya wajaba masu tsere su yi tsere a cikinsa, ta hanyar aikin da Allah zai yarda da shi, da barin abin baya so.**

**(27) Ana haxa wannan abin sha, wanda aka sanya shi a cikin mazubi mai liqaqqen baki da ruwan Tasnim.**

**(28) Idon ruwa ne a cikin Aljannah, wadda makusanta Allah suke sha daga gare ta, yana tataccen ruwa tsantsa, haka ma sauran Muminai ma suna sha daga wannan idon ruwa, amma wanda aka haxa shi da waninsa.**

**(29) Haqiqa waxanda suka yi laifi sakamakon kafircinsu, sun kasance suna yi wa Muminai dariya bisa izgilanci.**

**(30) Kuma idan suka wuce Muminai, sai sashensu ya riqa yin zunxe, yana mai izgili ga Muminai.**

**(31) Kuma idan suka koma ga iyalansu, sai su koma suna musu farin ciki da abin da suke kai na kafirci da izgili ga Muminai. (32) Kuma idan suka ga musulmai sai ka ji sun ce: "Haqiqa waxannan sun vacewa hanyar gaskiya, ta yadda suka bar addinin iyayensu. (33) Alhali kuma Allah bai wakilta su su riqa kiyaye ayyukan musulmai ba, ballantana su riqa faxar maganar da suke faxa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Haxarin zunubai ga zuciya. 2 - Hana kafirai ganin ubangijinsu a ranar alqiyama.**
**3 - Yin izgilanci ga masu addini wata siffa ce daga cikin siffofin kafirai.**

فَٱلۡيَوۡمَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنَ ٱلۡكُفَّارِ يَضۡحَكُونَ ٣٤ عَلَى
ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٣٥ هَلۡ ثُوِّبَ ٱلۡكُفَّارُ مَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ٣٦

ترتيبها ٨٣ — سُورَةُ الانْشِقَاقِ — آياتها ٢٥

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ثلاثة أرباع الحزب ٥٩
إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنشَقَّتۡ ١ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡأَرۡضُ مُدَّتۡ
٣ وَأَلۡقَتۡ مَا فِيهَا وَتَخَلَّتۡ ٤ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ٥ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلۡإِنسَٰنُ إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدۡحٗا فَمُلَٰقِيهِ ٦ فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ
كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ ٧ فَسَوۡفَ يُحَاسَبُ حِسَابٗا يَسِيرٗا ٨ وَيَنقَلِبُ
إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورٗا ٩ وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهۡرِهِۦ ١٠ فَسَوۡفَ
يَدۡعُواْ ثُبُورٗا ١١ وَيَصۡلَىٰ سَعِيرًا ١٢ إِنَّهُۥ كَانَ فِيٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورًا ١٣
إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ١٤ بَلَىٰٓۚ إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرٗا ١٥ فَلَآ أُقۡسِمُ
بِٱلشَّفَقِ ١٦ وَٱلَّيۡلِ وَمَا وَسَقَ ١٧ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا ٱتَّسَقَ ١٨
لَتَرۡكَبُنَّ طَبَقًا عَن طَبَقٖ ١٩ فَمَا لَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٢٠ وَإِذَا قُرِئَ
سجدة
عَلَيۡهِمُ ٱلۡقُرۡءَانُ لَا يَسۡجُدُونَۤ۩ ٢١ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُكَذِّبُونَ
٢٢ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا يُوعُونَ ٢٣ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢٤



**(34) To a ranar alqiyama waxanda suka yi imani zasu riqa yi wa kafirai dariya, kamar yadda kafirai suke musu dariya a duniya. (35) A kan gadaje masu ado, suna kallon abin da Allah ya tanadar musu na ni'ima dauwamammiya. (36) Tabbas an sakawa kafirai da azaba ta wulaqanci a kan ayyukan da suka gabatar a duniya marasa kyau.**

## Suratu Linshiqaq

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Suranta tashin alqiyama, ta yadda gaba xayan duniya zata ranqwafawa Allah Ubangijinta, tana mai lazimtar miqa wuya, da inkarin jayayya da musu da hakan.**

**Tafsir:** **(1) Idan sama ta tsage, saboda saukar Mala'iku daga cikinta.**
**(2) Kuma ta saurari Ubangijinta tana mai miqa wuya gare shi, kuma ya cancanta ta yi hakan.**
**(3) Idan qasa Allah ya miqar da ita, kamar yadda ake miqe fata. (4) Ta jefar da abin da yake cikinta, na dukiyoyi da matattu, ta rabu da su.**
**(5) Kuma ta saurari ubangijinta tana mai miqa wuya, kuma ya cancanta ta yi hakan. (6) Ya kai wannan mutum, tabbas kai mai aiki ne, kodai na alheri ko kuma na sharri, kuma tabbas zaka haxu da wannan aiki, don Allah ya saka maka a kanshi. Yayin da Allah ya ambaci aikin mutum a dunqule, sai kuma ya yi bayanin halin masu yin aikin a ranar alqiyama, ya ce:**
**(7) Amma wanda aka ba shi takardar ayyukansa a hannunsa na dama.**
**(8) To da sannu Allah zai yi masa hisabi mai sauqi, za a bijiro masa da ayyukansa, ba tare da an kama shi da laifinsa ba. (9) Kuma zai koma ga iyalansa yana cike da farin ciki.**
**(10) Amma duk wanda aka ba shi littafinsa a hannun hagunsa, kuma daga bayan bayansa.**
**(11) To da kansa zai kirawa kansa halaka.**
**(12) Kuma zai shiga wutar Jahannama, ya sha fama da zafinta.**
**(13) Haqiqa shi ya kasance a duniya a cikin iyalansa mai farin ciki ne da abin da yake kai na kafirci da savon Allah.**
**(14) Kuma haqiqa shi ya yi zaton ba zai dawo rayuwa ba, bayan mutuwarsa.**
**(15) Haka ne, tabbas sai Allah ya dawo da shi zuwa rayuwa, kamar yadda ya halicce shi a karo na farko. Haqiqa Ubangijinsa mai gani ne da duk abin da yake ciki, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma da sannu zai saka masa a kan ayyukansa. (16) Allah ya rantse da jaja-jajan da yake kasancewa a sararin samaniya bayan faxuwar rana.**
**(17) Kuma ya rantse da dare da abin da aka tattara a cikinsa.**
**(18) Da kuma wata idan ya haxu, ya cika, ya zama wata xan daren goma sha huxu.**
**(19) Ya ku mutane, tabbas zaku hau hali bayan hali, daga xigon maniyyi zuwa gudan jini, sannan gudan tsoka, sannan rayuwa sannan mutuwa, sannan tashi bayan mutuwa.**
**(20) To mene ne ya samu waxannan kafirai basa yin imani da Allah? Kuma basa yin imani da ranar lahira.**
**(21) Kuma idan aka karanta musu Alqur'ani basa yin sujjada ga Ubangijinsu?!**
**(22) Tabbas kafirai suna qaryata abin da Manzonsu ya zo musu da shi.**
**(23) Allah shi ne mafi sanin abin da qirazansu suka voye, babu wani aikinsu da yake vuya a gare shi.**
**(24) Ya kai wannan Manzo, ka ba su labarin azaba mai ciwo, da take jiran su.**

### Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yadda sama da qasa suke ranqwafawa Ubangijinsu. 2 - Kowane mutum mai aiki ne, kodai na alheri ko na sharri.**
**3 - Alamar rabauta a ranar alqiyama ita ce mutum ya karvi littafinsa a hannun damansa, kuma alamar tavewa ita ce ya karvi littafinsa a hannun hagu.**

إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونِۭ ٢٥

ترتيبها ٨٥ — سُورَةُ البُرُوجِ — آياتها ٢٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡبُرُوجِ ١ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡمَوۡعُودِ ٢ وَشَاهِدٖ وَمَشۡهُودٖ
٣ قُتِلَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأُخۡدُودِ ٤ ٱلنَّارِ ذَاتِ ٱلۡوَقُودِ ٥ إِذۡ هُمۡ عَلَيۡهَا
قُعُودٞ ٦ وَهُمۡ عَلَىٰ مَا يَفۡعَلُونَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ شُهُودٞ ٧ وَمَا نَقَمُواْ
مِنۡهُمۡ إِلَّآ أَن يُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ٨ ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ
فَتَنُواْ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَتُوبُواْ فَلَهُمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَ وَلَهُمۡ
عَذَابُ ٱلۡحَرِيقِ ١٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ
جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡكَبِيرُ ١١ إِنَّ بَطۡشَ
رَبِّكَ لَشَدِيدٌ ١٢ إِنَّهُۥ هُوَ يُبۡدِئُ وَيُعِيدُ ١٣ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلۡوَدُودُ ١٤
ذُو ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡمَجِيدُ ١٥ فَعَّالٞ لِّمَا يُرِيدُ ١٦ هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡجُنُودِ
١٧ فِرۡعَوۡنَ وَثَمُودَ ١٨ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي تَكۡذِيبٖ ١٩ وَٱللَّهُ مِن
وَرَآئِهِم مُّحِيطُۢ ٢٠ بَلۡ هُوَ قُرۡءَانٞ مَّجِيدٞ ٢١ فِي لَوۡحٖ مَّحۡفُوظِۭ ٢٢



**(25) Sai dai waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka aikata ayyuka nagari, to waxannan suna da lada wanda ba ya yankewa, shi ne Aljannah.**

# Suratul Buruj

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana qarfin Allah, da yadda ya mamaye komai, da mummunan narko ga masu qiyayya da Muminai, ta hanyar azaba mai tsanani.**

## Tafsir:

**(1) Allah ya yi rantsuwa da sama, wadda ta qunshi masaukan rana da wata da wasun su. (2) Kuma ya yi rantsuwa da ranar alqiyama, wadda ya yi alqawarin tattara halittu gaba xaya a cikinta. (3) Kuma ya yi rantsuwa da kowane mai yin shaida, kamar Annabi (S.A.W) da zai yi shaida ga al'ummarsa, da duk wanda za a yi shaidar a kansa, kamar al'umma, wadda zata yi shaida ga Annabinta. (4) An tsinewa waxanda suka yi qaton rami a bayan qasa. (5) Suka rura wuta a cikinsa, sannan suka jefa Muminai a cikin wannan rami a raye. (6) Yayin da suka kasance a zaune bakin wannan rami, wanda yake cike da wuta. (7) Kuma su, dangane da abin da suke aikatawa muminai na azaba masu shaida ne, saboda sun halacci wurin da hakan yake faruwa.**

**(8) Waxannan kafirai ba wani abu Muminai suka yi musu ba face sun yi imani da Allah Mabuwayi, wanda ba a rinjayar sa, kuma abin yabo a kowane hali. (9) Shi ne wanda shi kaxai yake da mulkin sammai da mulkin qassai, kuma mai ganin dukkan komai ne, babu abin da yake vuya a gare shi daga al'amuran bayinsa.**

**(10) Haqiqa waxanda suka azabtar da Muminai maza da mata da wuta, domin su kautar da su ga barin imani da Allah shi kaxai, sannan basu tuba zuwa ga Allah daga laifukansu ba, to suna da azabar wutar Jahannama a ranar alqiyama, kuma suna da azabar wuta mai quna, sakamakon abin da suka aikatawa muminai, na qona su da wuta.**

**(11) Haqiqa waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi ayyuka nagari, suna da Aljannatai waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu da bishiyoyinsu, wannan sakamakon da aka tanadar musu shi ne babban rabon da ba rabon da ya kai shi. (12) Haqiqa kamun Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - ga azzalumi yana da tsanani, koda kuwa ya jinkirta masa zuwa wani xan lokaci. (13) Haqiqa shi ne wanda yake qagar halitta da azaba, sannan kuma ya dawo da su. (14) Shi ne mai yawan gafara ga zunuban waxanda suka tuba gare shi daga cikin bayinsa, kuma yana son waliyyansa masu tsoronsa. (15) Shi ma'abocin al'arshi mai girma ne.**

**(16) Mai yawan aikata abin da ya ga dama ne, na yin afuwa ga zunuban bayinsa, kuma mai yin uquba ne ga wanda ya ga dama, babu mai yi masa dole (S.W.T). (17) Ya kai wannan Manzo, shin labarin rundunar da suka taru domin yaqar gaskiya, da hana yaxuwarta ya zo maka?!. (18) Fir'auna da Samudawa mutanen Annabi Salihu (A.S).**

**(19) Ba wai don ba su samu labaran al'ummun da aka halakar gabaninsu ba ne, yasa suka qi yin imani, kawai dai suna qaryata abin da Manzonsu ya zo musu da shi ne don bin son zuciyarsu.**

**(20) Amma Allah yana sane da ayyukansu ta ko'ina, kuma yana qididdige su, babu abin da yake kuvuce masa, kuma zai yi musu sakayya a kansu. (21) Alqur'ani ba waqe ba ne, ba kuma surkulle ba ne, kamar yadda masu qaryatawa suke faxa. A'a shi Alqur'ani ne mai girma.**

**(22) A cikin allo abin kiyayewa daga canjawa ko juyawa, ko ragewa ko qarawa (Wato Lauhul Mahfuz).**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Jarrabawa ga mumini tana kasancewa gwargwadon imaninsa.**

**2 - Fifita kuvutar imani a kan kuvutar gangar jiki, yana daga cikin alamomin kuvuta a ranar alqiyama.**

**3 - Tuban da ya cika sharuxansa, yana kankare laifukan da suka gabace shi.**

سُورَةُ الطَّارِقِ
آياتها ١٧ — ترتيبها ٨٦

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالسَّمَاءِ وَالطَّارِقِ ﴿١﴾ وَمَا أَدْرَاكَ مَا الطَّارِقُ ﴿٢﴾ النَّجْمُ الثَّاقِبُ
﴿٣﴾ إِن كُلُّ نَفْسٍ لَّمَّا عَلَيْهَا حَافِظٌ ﴿٤﴾ فَلْيَنظُرِ الْإِنسَانُ مِمَّ خُلِقَ ﴿٥﴾
خُلِقَ مِن مَّاءٍ دَافِقٍ ﴿٦﴾ يَخْرُجُ مِن بَيْنِ الصُّلْبِ وَالتَّرَائِبِ ﴿٧﴾ إِنَّهُ عَلَىٰ
رَجْعِهِ لَقَادِرٌ ﴿٨﴾ يَوْمَ تُبْلَى السَّرَائِرُ ﴿٩﴾ فَمَا لَهُ مِن قُوَّةٍ وَلَا نَاصِرٍ
﴿١٠﴾ وَالسَّمَاءِ ذَاتِ الرَّجْعِ ﴿١١﴾ وَالْأَرْضِ ذَاتِ الصَّدْعِ ﴿١٢﴾ إِنَّهُ
لَقَوْلٌ فَصْلٌ ﴿١٣﴾ وَمَا هُوَ بِالْهَزْلِ ﴿١٤﴾ إِنَّهُمْ يَكِيدُونَ كَيْدًا ﴿١٥﴾
وَأَكِيدُ كَيْدًا ﴿١٦﴾ فَمَهِّلِ الْكَافِرِينَ أَمْهِلْهُمْ رُوَيْدًا ﴿١٧﴾

سُورَةُ الأَعْلَى
آياتها ١٩ — ترتيبها ٨٧

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

سَبِّحِ اسْمَ رَبِّكَ الْأَعْلَى ﴿١﴾ الَّذِي خَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٢﴾ وَالَّذِي قَدَّرَ فَهَدَىٰ الحزب ٦٠
﴿٣﴾ وَالَّذِي أَخْرَجَ الْمَرْعَىٰ ﴿٤﴾ فَجَعَلَهُ غُثَاءً أَحْوَىٰ ﴿٥﴾ سَنُقْرِئُكَ
فَلَا تَنسَىٰ ﴿٦﴾ إِلَّا مَا شَاءَ اللَّهُ إِنَّهُ يَعْلَمُ الْجَهْرَ وَمَا يَخْفَىٰ ﴿٧﴾ وَنُيَسِّرُكَ
لِلْيُسْرَىٰ ﴿٨﴾ فَذَكِّرْ إِن نَّفَعَتِ الذِّكْرَىٰ ﴿٩﴾ سَيَذَّكَّرُ مَن يَخْشَىٰ ﴿١٠﴾



# Suratux Xariq

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana kulawar Allah ga bayinsa, da kuma ikonsa da ya kai matuqa.**

## Tafsir:

**(1) Allah ya rantse da sama, kuma ya rantse da tauraron da yake zuwa da daddare. (2) Ya kai wannan Manzo, mene ne ya sanar da kai lamarin wannan tauraro mai girma?! (3) Shi ne tauraron da yake keta sama da tsananin haskensa?. (4) Babu wata rai face Allah ya wakilta mata wani Mala'ika wanda yake kiyaye mata ayyukanta, domin yin hisabi a ranar alqiyama. (5) Don haka mutum ya yi la'akari daga me Allah ya halicce shi, domin ikon Allah da gazawar xan Adam su bayyana a gare shi,. (6) Allah ya halicce shi daga wani ruwa mai tunkuxar juna, wanda ake zuba shi a cikin mahaifa. (7) Wannan ruwa yana fitowa daga qashin gadon bayan namiji, da kuma haqarqarin qirji. (8) Haqiqa Allah (S.W.T) da ya halicce shi daga wannan wulaqantaccen ruwan, mai iko ne a kan tashin sa bayan mutuwarsa, ya komo rayayye, domin yi masa hisabi da sakayya. (9) A ranara da ake jarraba sirrin halitta, sai a bayyanar da abubuwan da zukata suke voyewa na niyya da qudurce- qudurce, da ma wasun su, sai nagari daga ciki ya bayyana daga lalatacce. (10) Mutum a wannan rana ba shi da wani qarfi da zai kare kansa daga azabar Allah da shi, ko wani mataimaki da zai taimake shi. (11) Allah ya rantse da sama ma'abociyar zubar da ruwa, domin daga cikinta ne yake sauka lokaci bayan lokaci. (12) Kuma ya rantse da qasa, wadda take kecewa, tsiro da shuka da bishiyoyi su fito daga cikinta. (13) Tabbas wannan Alqur'ani wanda aka saukarwa Annabi Muhammad (S.A.W) Magana ce da take rabewa tsakanin gaskiya da vata, da kuma gaskiya da qarya. (14) Kuma ba wasa ba ne, ba wargi ba ne, a'a shi gaskiya ne tsantsa. (15) Haqiqa waxanda suke qaryata abin da Manzonsu ya zo da shi, suna shirya makirci, makirci mai yawa, don su mayar da da'awar Manzon, su lalata ta. (16) Ni kuma ina shirya yadda zan warware makircinsu, don bayyana addini da kawar da varna. (17) Don haka - Ya kai wannan Manzo - ka saurarawa waxannan kafirai, ka saurara musu xan kaxan, kada ka yi gaggawar a halakar da su, ko kuma a azabtar da su.**

# Suratul A'a'la

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Tunatar da zukata babbar baiwar da Allah ya yi musu, da kuma sa zuciya ta rataya da rayuwar lahira, da raba ta da duniya da abin da suke shafe ta.**

**Tafsir:** **(1) Ka tsarkake Ubangijinka, wanda ya xaukaka a kan halittarsa, kana mai ambaton sunansa a lokacin da ka tuna shi, kuma kake girmama shi. (2) Wanda ya halicci mutum daidai, ya kuma daidaita tsayuwarsa. (3) Shi ne wanda ya tsara halittu, ta fuskar jinsinsu, nau'insu, siffarsu, kuma ya shiryar da kowane abin halitta zuwa ga abin da ya dace da shi. (4) Shi ne wanda ya fitar da abin da dabbobinku suke kiwo da shi daga cikin qasa. (5) Ya sanya shi karmami, busasshe, wanda ya karkata zuwa ga launin baqi, bayan ya kasance xanye kore fatau. (6) Ya kai wannan Manzo da sannu zamu karantar da kai Alqur'ani, kuma mu tara maka shi a cikin qirjinka, ba zaka manta shi ba, don haka kada ka riqa riga Mala'ika Jibrilu a wajen karatu, kamar yadda kake yi, don kwaxayin kada ka manta shi. (7) Sai dai abin da Allah ya ga damar ka manta shi daga ciki, saboda wata hikima. Haqiqa shi Allah (S.W.T) ya san me ake bayyanawa da kuma abin da ake voyewa, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu. (8) Kuma zamu sauwaqa maka aiki da abin da Allah ya yarda shi, na daga ayyukan da suke shigar da mutum Aljannah. (9) Don haka ka yi wa mutane wa'azi da wahayin da muke yi maka na Alqur'ani, kuma ka tunatar da su matuqar za a ji wa'azinka. (10) Da sannu wanda yake tsoron Allah zai amfana da wa'azinka, domin shi ne wanda yake amfanuwa da wa'azi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Mala'iku suna kiyaye mutum da ayyukansa na alheri da na sharri, domin a yi masa hisabi a kansu. 2 - Raunin makircin kafirai idan aka kwatanta da tanadin da Allah yake yi musu, lokacin da suke yin makirci. 3 - Tsoron Allah yana sa mutum ya wa'azantu.**

وَيَتَجَنَّبُهَا ٱلۡأَشۡقَى ١١ ٱلَّذِي يَصۡلَى ٱلنَّارَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ١٢ ثُمَّ لَا يَمُوتُ
فِيهَا وَلَا يَحۡيَىٰ ١٣ قَدۡ أَفۡلَحَ مَن تَزَكَّىٰ ١٤ وَذَكَرَ ٱسۡمَ رَبِّهِۦ فَصَلَّىٰ ١٥
بَلۡ تُؤۡثِرُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ١٦ وَٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓ ١٧ إِنَّ
هَٰذَا لَفِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٨ صُحُفِ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ١٩

## سُورَةُ الغَاشِيَةِ

آياتها ٢٦ — ترتيبها ٨٨

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡغَٰشِيَةِ ١ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ٢ عَامِلَةٞ
نَّاصِبَةٞ ٣ تَصۡلَىٰ نَارًا حَامِيَةٗ ٤ تُسۡقَىٰ مِنۡ عَيۡنٍ ءَانِيَةٖ ٥ لَّيۡسَ
لَهُمۡ طَعَامٌ إِلَّا مِن ضَرِيعٖ ٦ لَّا يُسۡمِنُ وَلَا يُغۡنِي مِن جُوعٖ ٧ وُجُوهٞ
يَوۡمَئِذٖ نَّاعِمَةٞ ٨ لِّسَعۡيِهَا رَاضِيَةٞ ٩ فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٖ ١٠ لَّا تَسۡمَعُ
فِيهَا لَٰغِيَةٗ ١١ فِيهَا عَيۡنٞ جَارِيَةٞ ١٢ فِيهَا سُرُرٞ مَّرۡفُوعَةٞ ١٣ وَأَكۡوَابٞ
مَّوۡضُوعَةٞ ١٤ وَنَمَارِقُ مَصۡفُوفَةٞ ١٥ وَزَرَابِيُّ مَبۡثُوثَةٌ ١٦ أَفَلَا يَنظُرُونَ
إِلَى ٱلۡإِبِلِ كَيۡفَ خُلِقَتۡ ١٧ وَإِلَى ٱلسَّمَآءِ كَيۡفَ رُفِعَتۡ ١٨ وَإِلَى
ٱلۡجِبَالِ كَيۡفَ نُصِبَتۡ ١٩ وَإِلَى ٱلۡأَرۡضِ كَيۡفَ سُطِحَتۡ ٢٠
فَذَكِّرۡ إِنَّمَآ أَنتَ مُذَكِّرٞ ٢١ لَّسۡتَ عَلَيۡهِم بِمُصَيۡطِرٍ ٢٢



**(11) Kuma kafiri yana nisantar wa'azi, yana guje masa, saboda shi ne mafi tavewar mutane a lahira, saboda shigarsa wuta. (12) Shi ne wanda zai shiga babbar wuta ta lahira, kuma ya sha fama da zafinta har abada. (13) Sannan a dauwamar da shi a cikin wuta, ta yadda ba zai mutu a cikinta ba, ballantana ya huta da abin da yake fama da shi na azaba, kuma ba zai rayu ba, rayuwa ta jin daxi da karamci. (14) Haqiqa wanda ya tsarkaka daga shirka da savon Allah ya rabauta da abin nema. (15) Kuma ya ambaci ubangijinsa da nau'ikan abin da ya shar'anta na zikiri, kuma ya gabatar da sallah a kan siffar da aka nemi ya yi ta a kai. (16) Kawai dai kuna gabatar da rayuwar duniya ne, kuna fifita ta a kan rayuwar lahira, duk da abin da yake tsakaninsu na bambanci mai girma. (17) Kuma wallahi lahira ta fi duniya da abin da yake cikinta na kayan jin daxi alheri da falala, kuma ta fita dauwama, domin abin da yake cikinta na ni'ima baya yankewa har abada. (18) Haqiqa wannan abin da muka ambata muku, na labarai da umarni wallahi suna cikin takardun da aka saukar gabaninka. (19) Su ne takardun da aka saukarwa Annabi Ibrahim da Musa, tsira da aminci su tabbata a gare su.**

# Suratul Gashiyah

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Tunatar da zukata kallon abin da yake nuna ikon Allah, cikin azaba da ni'ima, da bayanin dalilan da suke tabbatar da haka daga ayoyin Allah waxanda ake gani, domin zukata su cika da kwaxayin rahamar Allah, da tsoron azabarsa.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Manzo, shin labarin tashin alqiyama ya zo maka, wadda take lulluve mutane da tashin hankalinta?!. (2) Mutane a ranar alqiyama, kodai 'yan wuta, ko kuma 'yan Aljannah. Fuskokin 'yan wuta zasu kasance a cikin qasqanci. (3) A gajiye, a wahale cikin sarqoqin da ake jan su da su, da sasarin da aka xaure su da su. (4) Waxannan fuskokin zasu shiga wata wuta mai zafi, zasu sha fama da zafinta. (5) Kuma ana shayar da su da wani idon ruwa mai tsananin zafi. (6) Basu da wani abinci da suke ci, sai mafi munin abinci, mafi xoyi, daga wani tsiro da ake kiransa Shibriq, wanda idan ya bushe sai ya zama guba. (7) Mai cin sa baya qiba, kuma baya kawar masa da yunwar da yake ji. (8) Amma fuskokin 'yan Aljannah a wannan rana suna cikin ni'ima da walwala da farin ciki, saboda abin da suka gamu da shi na ni'ima. (9) Waxannan fuskoki sun yarda da ayyukan da suka aikata a duniya, domin sun samu ladan ayyukansu a ajiye, an ninninka musu shi. (10) Suna cikin Aljannah mai daraja, a wani wuri maxaukaki. (11) Ba zaka tava jin maganar banza ko yasasshen zance a cikin gidan Aljannah ba, ballantana ka ji kalmar da Allah ya haramta. (12) A cikin wannan Aljannar akwai idanuwan ruwa da suke vuvvugowa, suna sarrafa su yadda suka ga dama. (13) Kuma a cikinta akwai gadaje maxaukaka. (14) Da kofuna a zube, an shirya su don sha da su. (15) A cikinta akwai matasai (Pillow) an jera su, wasu a gefen wasu. (16) Kuma a cikinta akwai shimfixu waxanda aka shimfixa su, nan da can. Yayin da Allah ya ambaci bambancin halin 'yan wuta da 'yan Aljannah a lahira, sai ya janyo hankalin kafirai zuwa ga abin da zai nuna musu ikon Allah Mahalicci, da kyawun halittarsa, domin hakan ya zama dalilin da zasu yi imani, su shiga Aljannah, su zamo daga cikin masu rabauta, Allah ya ce: (17) Yanzu ba zasu kalli - kallo na lura – zuwa ga raquma ba, yaya Allah ya halicce su, kuma ya hore su ga 'yan Adam?! (18) Kuma su kalli sama, ta yaya Allah ya xaga ta, ta zama rufi a samansu, wanda aka kiyaye, baya faxowa a kansu?!. (19) Kuma su kalli duwatsu ta yaya Allah ya kafa su, ya riqe qasa da su, don kada ta motsa da mutane?! (20) Kuma su kalli qasa, ta yaya Allah ya shimfixa ta, kuma ya sanyata ta dace da zaman mutane a doron ta?!. Yayin da Allah ya ja hankalinsu zuwa abubuwan da zasu nuna musu ikon Allah Maxaukakin sarki, sai kuma ya nusar da Manzonsa ya ce: (21) Ya kai wannan Manzo, ka yi wa'azi ga waxannan, ka tsoratar da su azabar Allah, domin kai mai gargaxi ne kawai, babu abin da ake nema a wurinka sai yi musu wa'azi, amma datar da su ga yin imani, to wannan yana hannun Allah shi kaxai.**

**(22) Kuma ba'a xora ka a kansu ba, ballantana ka tilasta musu karvar imani.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Muhimmancin tsarkake zukata daga dukkan datti na fili da na voye. 2 - Kafa hujja da halittu akan samuwar Allah Mahalicci da girmansa. 3 - Aikin mai da'awa shi ne kira zuwa ga Allah, ba wai tilasta mutane a kan sai sun shiriya ba, domin shiriya tana hannun Allah.**

إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ٢٣ فَيُعَذِّبُهُ ٱللَّهُ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَكْبَرَ ٢٤
إِنَّ إِلَيْنَآ إِيَابَهُمْ ٢٥ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ٢٦

## سُورَةُ الفَجْرِ

ترتيبها ٨٩ — آياتها ٣٠

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْفَجْرِ ١ وَلَيَالٍ عَشْرٍ ٢ وَٱلشَّفْعِ وَٱلْوَتْرِ ٣ وَٱلَّيْلِ إِذَا يَسْرِ ٤
هَلْ فِى ذَٰلِكَ قَسَمٌ لِّذِى حِجْرٍ ٥ أَلَمْ تَرَ كَيْفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ٦
إِرَمَ ذَاتِ ٱلْعِمَادِ ٧ ٱلَّتِى لَمْ يُخْلَقْ مِثْلُهَا فِى ٱلْبِلَٰدِ ٨ وَثَمُودَ ٱلَّذِينَ
جَابُوا۟ ٱلصَّخْرَ بِٱلْوَادِ ٩ وَفِرْعَوْنَ ذِى ٱلْأَوْتَادِ ١٠ ٱلَّذِينَ طَغَوْا۟ فِى
ٱلْبِلَٰدِ ١١ فَأَكْثَرُوا۟ فِيهَا ٱلْفَسَادَ ١٢ فَصَبَّ عَلَيْهِمْ رَبُّكَ سَوْطَ
عَذَابٍ ١٣ إِنَّ رَبَّكَ لَبِٱلْمِرْصَادِ ١٤ فَأَمَّا ٱلْإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ
رَبُّهُۥ فَأَكْرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّىٓ أَكْرَمَنِ ١٥ وَأَمَّآ إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ
فَقَدَرَ عَلَيْهِ رِزْقَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّىٓ أَهَٰنَنِ ١٦ كَلَّا ۖ بَل لَّا تُكْرِمُونَ
ٱلْيَتِيمَ ١٧ وَلَا تَحَٰٓضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ١٨ وَتَأْكُلُونَ
ٱلتُّرَاثَ أَكْلًا لَّمًّا ١٩ وَتُحِبُّونَ ٱلْمَالَ حُبًّا جَمًّا ٢٠ كَلَّآ إِذَا
دُكَّتِ ٱلْأَرْضُ دَكًّا دَكًّا ٢١ وَجَآءَ رَبُّكَ وَٱلْمَلَكُ صَفًّا صَفًّا ٢٢



**(23) Amma wanda ya bada baya ga barin imani, ya kafircewa Allah da Manzonsa. (24) Sai Allah ya azabta shi a ranar alqiyama azaba mai girma, ita ce ya shigar da shi wutar Jahannama, yana mai dauwama a cikinta. (25) Haqiqa zuwa gare mu, mu kaxai, makomarsu take bayan mutuwarsu. (26) Sannan zuwa gare mu ne kaxai hisabin ayyukansu yake, ba naka ba ne, ba na waninka ba ne.**

# Suratul Fajri

An Saukar Da Ita A Makka

**Daga Manufofin Surar:** **Bayanin abubuwan da suke nuna girma da ikon Allah a cikin wannan duniya, da bayanin halayen mutum, da bayanin qarshen waxanda suka ruxu da wannan rayuwa.**

**Tafsir:** **(1) Allah Maxaukakin Sarki yana rantsuwa da alfijir. (2) Kuma ya rantse da darurrukan goman farko na watan zul-hijja. (3) Kuma ya rantse da abubuwa masu bibiyu da masu xai-xai. (4) Kuma ya rantse da dare idan ya zo, sannan ya bada baya. Dalilin waxannan rantse-rantse shi ne, tabbas za a saka muku a kan ayyukanku. (5) Shin a cikin abubuwan nan da aka ambata akwai abin rantsuwa ga mai hankali?. (6) Ya kai wannan Manzo baka ga yadda Ubangijinka ya aikata wa Adawa ba, mutanen Annabi Hudu, yayin da suka qaryata Manzonsa?. (7) Qabilar Adawa waxanda suke dangantuwa zuwa ga kakansu Iram, ma'abocin tsawo. (8) Qabilar da Allah bai halicci kwatankwacinta a wasu garuruwa ba.**

**(9) Baka ga yadda Ubangijinka ya aikata wa Samudawa ba, mutanen Annabi Salihu, waxanda suka tsaga duwatsu, suka yi gidaje a garin Hijri. (10) Baka ga yadda Ubangijinka ya aikata wa Fir'auna ba, wanda yake da turaku (Wurin xaure mutane) da yake azabtar da mutane da su. (11) Dukkan waxannan sun qetare iyaka, wajen girman kai da zalunci, kowa ya aikata hakan a garin da yake. (12) Suka yawaita varna ta hanyar abin da suka yaxa na kafirci da zalunci. (13) Sai Allah ya xanxana musu azabarsa mai tsanani, ya tunvuke su daga bayan qasa.**

**(14) Haqiqa Ubangijinka – ya kai wannan Manzo – yana jiran ayyukan mutane, kuma yana lura da su, don ya sakawa wanda ya kyautata da Aljannah, wanda ya munana kuma da wuta. Yayin da al'ummun da Allah ya halakar, sun kasance Allah ya yi musu ni'imar jin daxi da qarfi, sai Allah ya bayyana cewa samun ni'ima ba dalili ba ne, da yake nuna Allah ya yarda da su, Allah ya ce: (15) Amma shi mutum, yana daga cikin xabi'arsa, idan Ubangijinsa ya jarrabe shi, ya girmama shi, ya yi masa ni'imar dukiya, da 'ya'ya, da matsayi, sai ya yi zaton wannan girmamawa ce gare shi a wajen Allah, sai ya riqa cewa: "Ubangijina ya girmama ni, saboda na cancanta da girmamawarsa".**

**(16) Amma idan ya jarrabe shi, ya quntata arzikinsa, sai ya yi zaton saboda wulaqantarsa ne a wurin Ubangijinsa, don haka sai ya riqa cewa: "Ubangijina ya wulaqanta ni". (17) Kayya, lamarin ba kamar yadda mutum yake zato ba ne, na cewa ni'ima tana nuna Allah ya yarda da bawa, wahala kuma tana nuna wulaqantar bawa a wajen Ubangiji, kawai abin yake faruwa shi ne, ba kwa girmama maraya, ta hanyar abin da Allah ya baku na arziki.**

**(18) Sashenku baya kwaxaitar da sashe a kan ciyar da faqiri, wanda bai da abin da zai ci. (19) Kuna cin haqqoqin raunana, mata da marayu, ci mai tsanani, ba tare da duban ko ya hallata ba. (20) Kuna son dukiya so mai yawa, don haka kuke rowar ciyar da ita a kan tafarkin Allah, saboda yadda kuke son ta.**

**(21) Bai dace a ce wannan ne aikinku ba. Ku tuna idan aka motsa qasa motsawa mai tsanani, aka girgizata.**

**(22) Ubangijinka ya zo – Ya kai wannan Manzo – don yin hukunci tsakanin bayi. kuma Mala'iku suka zo sahu-sahu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Falalar goman farko na watan zul-hijja, a kan sauran kwanakin shekara. 2 - Tabbatar da Allah zai zo ranar alqiyama, irin zuwan da ya dace da shi, ba tare da kamantawa ba, ko misaltawa, ko kore ma'anar lafazin ba. 3 - Mumini idan aka jarrabe shi sai ya yi haquri, idan kuma aka ba shi, sai ya godewa Allah.**

وَجِاْيٓءَ يَوۡمَئِذِۭ بِجَهَنَّمَۚ يَوۡمَئِذٖ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ وَأَنَّىٰ
لَهُ ٱلذِّكۡرَىٰ ٢٣ يَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي قَدَّمۡتُ لِحَيَاتِي ٢٤ فَيَوۡمَئِذٖ
لَّا يُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٥ وَلَا يُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٦ يَٰٓأَيَّتُهَا
ٱلنَّفۡسُ ٱلۡمُطۡمَئِنَّةُ ٢٧ ٱرۡجِعِيٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِيَةٗ مَّرۡضِيَّةٗ ٢٨
فَٱدۡخُلِي فِي عِبَٰدِي ٢٩ وَٱدۡخُلِي جَنَّتِي ٣٠

آياتها ٢٠ — سُورَةُ البَلَدِ — ترتيبها ٩٠

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ربع الحزب ٦٠
لَآ أُقۡسِمُ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ١ وَأَنتَ حِلُّۢ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ٢ وَوَالِدٖ وَمَا وَلَدَ
٣ لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِي كَبَدٍ ٤ أَيَحۡسَبُ أَن لَّن يَقۡدِرَ عَلَيۡهِ
أَحَدٞ ٥ يَقُولُ أَهۡلَكۡتُ مَالٗا لُّبَدًا ٦ أَيَحۡسَبُ أَن لَّمۡ يَرَهُۥٓ أَحَدٌ
٧ أَلَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ عَيۡنَيۡنِ ٨ وَلِسَانٗا وَشَفَتَيۡنِ ٩ وَهَدَيۡنَٰهُ
ٱلنَّجۡدَيۡنِ ١٠ فَلَا ٱقۡتَحَمَ ٱلۡعَقَبَةَ ١١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡعَقَبَةُ ١٢
فَكُّ رَقَبَةٍ ١٣ أَوۡ إِطۡعَٰمٞ فِي يَوۡمٖ ذِي مَسۡغَبَةٖ ١٤ يَتِيمٗا ذَا مَقۡرَبَةٍ
١٥ أَوۡ مِسۡكِينٗا ذَا مَتۡرَبَةٖ ١٦ ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَوَاصَوۡاْ
بِٱلصَّبۡرِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡمَرۡحَمَةِ ١٧ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ ١٨

**(23) A wannan rana aka zo da wutar Jahannama, tana da linzami dubu saba'in, a kan kowane linzami akwai Mala'ika dubu saba'in suna jan ta. A wannan rana mutum zai tuna sakacin da ya yi a vangaren bautawa Allah, amma ta ina wannan tunanin zai masa amfani a wannan rana? Domin ranar sakamako ce, ba ranar aiki ba.**
**(24) Saboda tsananin nadama mutum zai ce, Kaicona, ina ma na gabatar da ayyuka nagari saboda rayuwata ta lahira, wadda ita ce rayuwa ta haqiqa. (25) A wannan rana ba wanda zai yi azaba kamar azabar Allah, saboda azabar Allah ta fi tsanani, kuma ta fi wanzuwa. (26) Ba wani wanda zai yi xauri a cikin sarqa, kamar yadda Allah zai xaure kafirai. Yayin da Allah ya ambaci sakamakon kafirai, sai ya ambaci sakamakon muminai ya ce: (27) Amma shi ran mumini za a ce da shi yayin mutuwa, da kuma ranar alkiyama: "Yake wannan rai, mai nutsuwa da imani, da aiki nagari". (28) "Ki koma zuwa ga Ubangijinki, kina mai yarda da abin da zaki samu na lada mai yawa, kuma abar yadda a wajen Allah, saboda abin da kike da shi na aiki nagari". (29) "Ki shiga cikin bayina nagartattu". (30) "Ki shiga Aljannata tare da su, wadda na tanadar musu ita".**

# Suratul Balad

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton halin da mutum yake kasancewa a ciki, tsakanin wahalhalun kafirci da azaba, da kuma hawa tsanin rahama da imani a duniya da lahira.**

**Tafsir: (1) Allah ya rantse da gari mai alfarma, wanda shi ne Makkah. (2) Kuma kai - Ya wannan Manzo – abin da kake aikatawa a cikinta halal ne, na kashe wanda ya cancanta a kashe, ko kama wanda ya cancanta a kama.**
**(3) Kuma Allah ya rantse da mahaifin mutum, kuma ya rantse da abin da ya fito da tsatsonsa na 'ya'ya.**
**(4) Haqiqa mun halicci mutum a cikin wahala da gajiya, saboda abubuwan da yake fama da su na wahalhalu a cikin duniya. (5) Shin yanzu mutum yana zaton idan ya aikata savo, babu wanda yake da iko a kansa, babu wanda zai kama shi, koda Ubangijinsa ne wanda ya halicce shi?! (6) Sai ka ji yana cewa: "Na ciyar da dukiya mai yawa, wata na bin wata". (7) Shin yanzu wannan mai yin fariyar da abin da ya ciyar, yana zaton Allah baya ganinsa?! Kuma ba zai yi masa hisabi a kan dukiyarsa ba, daga ina ya samo ta? Kuma a kan me ya ciyar da ita?!.**
**(8) Shin bamu sanya masa idanuwa guda biyu ba, waxanda yake gani da su?! (9) Da kuma harshe da levva guda biyu, waxanda yake yin magana da su?! (10) Kuma muka sanar da shi hanyar alheri, da kuma hanyar vata?!**
**(11) Kuma aka neme shi da ya tsallake tudun da yake tsakaninsa da Aljannah, ya wuce shi, ya tsallake shi.**
**(12) Ya kai wannan Manzo, me ya sanar da kai wanne tudu ne yake wajibi a kansa ya tsallake shi don ya shiga Aljannah? (13) Shi ne 'yanta wuyaye, namiji ne ko mace. (14) Ko kuma ya ciyar a ranar da ake yunwa, wadda abinci ya yi kaxan a cikinta. (15) Ya ciyar da yaron da ya rasa mahaifinsa (maraya) wanda da akwai 'yan uwantaka a tsakaninsu. (16) Ko kuma talaka, wanda ba shi da abin da ya mallaka.**
**(17) Sannan ya kasance daga cikin waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yiwa juna wasiyya da haquri a kan xa'ar Allah, da barin savonsa, da haquri a kan bala'i, kuma suka yi wa juna wasiyya da tausayawa bayin Allah.**
**(18) Waxanda suka siffantu da waxancan siffofi su ne ma'abota hannun dama.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - 'Yanta bayi, da ciyar da mabuqata a lokacin tsanani, da yin imani da Allah, da yi wa juna wasici da haquri da tausayi, suna cikin sabubban shiga Aljannah. 2 - Yana daga dalilan Annabta, labarin da ya bayar cewa garin Makkah zai kasance halal a gare shi a wani xan lokaci a cikin yini. 3 - Yayin da Allah ya quntata hanyar bauta, sai ya yalwata hanyar samun 'yanci, ya sanya 'yantawa daga cikin ayyukan ibada da samun kaffara.**

وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ ١٩ عَلَيۡهِمۡ نَارٞ مُّؤۡصَدَةُۢ ٢٠

سُورَةُ الشَّمۡسِ — آياتها ١٥ — ترتيبها ٩١

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلشَّمۡسِ وَضُحَىٰهَا ١ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ٢ وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا
٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰهَا ٤ وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ٥ وَٱلۡأَرۡضِ
وَمَا طَحَىٰهَا ٦ وَنَفۡسٖ وَمَا سَوَّىٰهَا ٧ فَأَلۡهَمَهَا فُجُورَهَا
وَتَقۡوَىٰهَا ٨ قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ٩ وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا
١٠ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِطَغۡوَىٰهَآ ١١ إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشۡقَىٰهَا ١٢ فَقَالَ لَهُمۡ
رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقۡيَٰهَا ١٣ فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمۡدَمَ
عَلَيۡهِمۡ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمۡ فَسَوَّىٰهَا ١٤ وَلَا يَخَافُ عُقۡبَٰهَا ١٥

سُورَةُ اللَّيۡلِ — آياتها ٢١ — ترتيبها ٩٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰ ١ وَٱلنَّهَارِ إِذَا تَجَلَّىٰ ٢ وَمَا خَلَقَ ٱلذَّكَرَ وَٱلۡأُنثَىٰٓ ٣
إِنَّ سَعۡيَكُمۡ لَشَتَّىٰ ٤ فَأَمَّا مَنۡ أَعۡطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ٥ وَصَدَّقَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٦
فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡيُسۡرَىٰ ٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ وَٱسۡتَغۡنَىٰ ٨ وَكَذَّبَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٩



(19) Waxanda suka kafirce wa ayoyinmu, waxanda aka saukar wa Manzonmu su ne ma'abota hannun hagu. (20) Kuma wuta rufaffiya ta tabbata a gare su ranar alqiyama, za a azabtar da su a cikinta.

## Suratus Shamsi

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Surar ta mayar da hankali akan bayyana ayoyin Allah, da ni'imominsa a bayan qasa, da mutane, domin tsarkake zukata, da kuma tsoratarwa daga savon Allah.

**Tafsir:** (1) Allah ya yi rantse da rana, kuma ya yi rantse da lokacin xagawarta bayan ta vullo daga mafaxarta. (2) Kuma ya rantse da wata, idan ya biyo gurbin rana bayan ta faxi. (3) Kuma ya rantse da yini, yayin da ya bayyana duk abin da yake bayan qasa da haskensa. (4) Kuma ya rantse da dare, yayin da yake lulluve bayan qasa, ya zama ya yi duhu. (5) Kuma ya rantse da sama, ya kuma rantse da gine-ginenta masu kyau. (6) Kuma ya rantse da qasa, ya kuma rantse da shimfixa ta, domin mutane su zauna a bayanta. (7) Kuma ya rantse da kowace rai, ya kuma rantse da yadda Allah ya halicce ta daidaitacciya. (8) Kuma ya fahimtar da ita, ba tare da an koya mata ba, mene ne sharri don ta nisance shi, kuma mene ne alheri don ta aikata shi. (9) Haqiqa ya rabauta da abin da yake nema, wanda ya tsarkake zuciyarsa, ta hanyar qawata ta da kyawawan xabi'u, da rabata da miyagun xabi'u. (10) Kuma Haqiqa duk wanda ya turbuxe zuciyarsa da laifi da savon Allah ya yi asara. Yayin da Allah ya ambaci asarar wanda ya turbuxe zuciyarsa da laifi da savon Allah, sai ya ambaci Samudawa a matsayin misali a kan hakan, ya ce: (11) Samudawa sun qaryata Manzonsu Salihu, saboda qetare iyakarsu cikin savon Allah, da yi masa laifi. (12) Lokacin da mafi rashin arziqinsu ya tashi bayan mutanensa sun kira shi. (13) Sai Manzon Allah Salihu (A.S) ya ce mu su: "Ku qyale taguwar Allah, da ranar shan ruwanta, kada ku cutar da ita". (14) Amma sai suka qaryata Manzonsu cikin lamarin taguwar, sai mafi tavewarsu ya kashe ta, tare da yardarsu da abin da ya aikata, don haka sai suka yi tarayya a cikin laifin, sai Allah ya game su da azabarsa, ya halakar da su ta hanyar tsawa, saboda laifukansu, kuma ya daidaita su a cikin uqubar, wadda ya halakar da su da ita. (15) Allah ya yi musu azabar da ya halakar da su, ba tare da yana jin tsoron abin da zai biyo baya ba.

## Suratul Laili

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Bayanin bambancin da yake tsakanin ayoyi, da rayuka, da ayyukansu, don nuna fifikon da yake tsakanin Muminai da Kafirai.

**Tafsir:** (1) Allah ya rantse da dare, lokacin da ya rufe abin da yake tsakanin sama da qasa da duhunsa. (2) Kuma ya rantse da yini, idan ya bayyana ya fito a fili. (3) Kuma ya rantse da halittarsa guda biyu, namiji da mace. (4) Ya ku mutane tabbas ayyukanku mabambanta ne, daga cikinsu akwai ayyuka nagari, waxanda suke zama sababin shiga Aljannah, kuma akwai munanan ayyuka, waxanda suke zama sababin shiga wuta. (5) Amma duk wanda ya bayar da abin da ya wajaba ya bayar, na zakka, da ciyarwa, da kaffara, kuma ya ji tsoron aikata abin da Allah ya hana. (6) Kuma ya gasgata abin da Allah ya yi masa alqawari na mayar masa da abin da ya bayar. (7) To da sannu zamu sauwaqe masa yin ayyuka nagari, da ciyarwa a kan tafarkin Allah. (8) Amma duk wanda ya yi rowar dukiyarsa, bai ciyar da ita cikin abin da ya wajaba a kansa ba, kuma ya wadatu da dukiyarsa ga barin Allah, kuma bai roqi Allah komai daga falalarsa ba. (9) Kuma ya qaryata abin da Allah ya yi masa alqawarinsa, na mayar masa da abin da ya ciyar, da bashi lada a kan ciyar da dukiyarsa a kan tafarkin Allah.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Muhimmancin tsarkake zuciya da tsaftace ta. 2 - Masu taimakekkeniya a kan savon Allah suna yin tarayya a cikin laifi. 3 - Zunubai sabubba ne na uqubar duniya. 4 - Kowa abin horewa ne ga abin da aka halicce shi dominsa. Don haka a cikin bayi akwai mai biyayya da mai savo.

فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْعُسْرَىٰ ١٠ وَمَا يُغْنِى عَنْهُ مَالُهُۥٓ إِذَا تَرَدَّىٰٓ ١١ إِنَّ عَلَيْنَا
لَلْهُدَىٰ ١٢ وَإِنَّ لَنَا لَلْـَٔاخِرَةَ وَٱلْأُولَىٰ ١٣ فَأَنذَرْتُكُمْ نَارًا تَلَظَّىٰ ١٤
لَا يَصْلَىٰهَآ إِلَّا ٱلْأَشْقَى ١٥ ٱلَّذِى كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ١٦ وَسَيُجَنَّبُهَا
ٱلْأَتْقَى ١٧ ٱلَّذِى يُؤْتِى مَالَهُۥ يَتَزَكَّىٰ ١٨ وَمَا لِأَحَدٍ عِندَهُۥ مِن نِّعْمَةٍ
تُجْزَىٰٓ ١٩ إِلَّا ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ رَبِّهِ ٱلْأَعْلَىٰ ٢٠ وَلَسَوْفَ يَرْضَىٰ ٢١

## سُورَةُ الضُّحَىٰ

ترتيبها ٩٣ — آياتها ١١

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلضُّحَىٰ ١ وَٱلَّيْلِ إِذَا سَجَىٰ ٢ مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ٣
وَلَلْـَٔاخِرَةُ خَيْرٌ لَّكَ مِنَ ٱلْأُولَىٰ ٤ وَلَسَوْفَ يُعْطِيكَ رَبُّكَ
فَتَرْضَىٰٓ ٥ أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَـَٔاوَىٰ ٦ وَوَجَدَكَ ضَآلًّا فَهَدَىٰ
٧ وَوَجَدَكَ عَآئِلًا فَأَغْنَىٰ ٨ فَأَمَّا ٱلْيَتِيمَ فَلَا تَقْهَرْ ٩
وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنْهَرْ ١٠ وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ١١

## سُورَةُ الشَّرْحِ

ترتيبها ٩٤ — آياتها ٨

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

نصف الحزب ٦٠ أَلَمْ نَشْرَحْ لَكَ صَدْرَكَ ١ وَوَضَعْنَا عَنكَ وِزْرَكَ ٢



**(10) To da sannu zamu sauwaqe masa aikata ayyukan sharri, kuma mu sanya aikata alheri ya yi masa wahala. (11) Kuma dukiyarsa da yake yin rowa da ita ba zata amfana masa komai ba, yayin da ya halaka, kuma ya shiga wuta. (12) Tabbas wajibi ne a kanmu, mu bayyana hanyar gaskiya daga vata. (13) Kuma tabbas rayuwar lahira da ta duniya tamu ce, muna sarrafa su yadda muka ga dama, kuma babu wani mai ikon hakan wadda ba mu ba. (14) Ya ku mutane ina tsoratar da ku wata wuta mai ci ganga ganga, mai ruruwa idan kun savawa Allah. (15) Babu wanda zai sha fama da zafin wannan wutar, sai mafi tavewa, wato kafiri. (16) Shi ne wanda ya qaryata abin da Manzo ya zo da shi, kuma ya bada baya ga barin kamanta umarnin Allah. (17) Kuma da sannu za a nesanta mafi tsoron Allah a cikin mutane daga shiga wannan wuta, wato Abubakar, Allah ya qara masa yarda. (18) Shi ne wanda yake ciyar da dukiyarsa a cikin ayyukan alheri, domin ya samu tsarkaka daga zunubai. (19) Kuma ba wai yana ciyar da abin da yake ciyarwa ba ne daga dukiyarsa, domin ya sakawa wani wata ni'ima da ya yi masa a baya. (20) Baya neman komai da abin da yake bayarwa, sai neman yardar Allah, Ubangijinsa Maxaukaki a kan dukkan halittarsa. (21) Kuma da sannu zai gamsu da abin da Allah zai ba shi na lada mai girma.**

# Suratud Dhuha

An saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton kulawar Allah ga Annabinsa (S.A.W) da kuma tuna masa baiwa ni'imar wahayi da aka yi masa, tare da dauwamar wannan ni'imar a gare shi, domin xebe masa kewa, da kuma tunatar da Muminai gabatar da godiya a kan hakan.**

**Tafsir:** **(1) Allah ya rantse da farkon yini. (2) Kuma ya rantse da dare, yayin da yayi duhu, mutane suka samu nutsuwa da barin kai-kawo. (3) Ya kai wannan Manzo, Ubangijinka bai barka ba, kuma bai yi fushi da kai ba, kamar yadda Mushirikai suke faxa, lokacin da wayahi ya yanke. (4) Kuma Wallahi gidan lahira ya fi maka alheri a kan duniya, saboda abin da yake cikinta na ni'ima dauwamammiya wadda bata yankewa. (5) Kuma da sannu Allah zai baka lada mai yawa, da al'ummar ka, har sai ka yarda da abin da ya ba ka, kuma ya bawa al'ummar ka. (6) Tabbas ya same ka, kana qarami, mahaifinka ya rasu, sai ya sanya maka makoma, ta yadda ya sa kakanka Abdulmuxxalib ya tausaya maka, sannan baffanka Abu Xalib. (7) Kuma ya same ka, baka da wani sani a kan imani ko Alqur'ani, sai ya sanar da kai daga cikinsu abin baka sani ba. (8) Kuma ya same ka talaka sai ya wadata ka. (9) Don haka kada ka munana mu'amalar wanda ya rasa mahaifinsa yana qarami, kuma kada ka qasqantar da shi. (10) Kuma kada yi tsawa ga mabuqaci mai roqo. (11) Ka godewa Allah ni'imar da ya yi maka, kuma ka yi bayaninta.**

# Suratus Sharhi

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton cikar ni'imar Allah ga Annabinsa (S.A.W) ta hanyar gusar masa da damuwa da qunci, da tsanani, da bayanin abin da yake kawo hakan.**

**Tafsir:** **(1) Haqiqa Allah ya yalwata maka qirjinka, ya sanya maka son karvar wahayi. (2) Kuma muka goge maka laifukanka.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Matsayin Annabi (S.A.W) a wurin Ubangijinsa, babu matsayin da ya kai shi. 2 - Godewa ni'ima, haqqin Allah ne akan bawa. 3 - Wajabcin tausayawa masu rauni da jin qansu.**

ٱلَّذِىٓ أَنقَضَ ظَهۡرَكَ ٣ وَرَفَعۡنَا لَكَ ذِكۡرَكَ ٤ فَإِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ٥
إِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ٦ فَإِذَا فَرَغۡتَ فَٱنصَبۡ ٧ وَإِلَىٰ رَبِّكَ فَٱرۡغَب ٨

## سُورَةُ التِّين
آياتها ٨ ترتيبها ٩٥

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلتِّينِ وَٱلزَّيۡتُونِ ١ وَطُورِ سِينِينَ ٢ وَهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ٱلۡأَمِينِ ٣
لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِىٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ ٤ ثُمَّ رَدَدۡنَٰهُ أَسۡفَلَ سَٰفِلِينَ
٥ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٦
فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعۡدُ بِٱلدِّينِ ٧ أَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَحۡكَمِ ٱلۡحَٰكِمِينَ ٨

## سُورَةُ العَلَق
آياتها ١٩ ترتيبها ٩٦

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱقۡرَأۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلَّذِى خَلَقَ ١ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِنۡ عَلَقٍ ٢ ٱقۡرَأۡ
وَرَبُّكَ ٱلۡأَكۡرَمُ ٣ ٱلَّذِى عَلَّمَ بِٱلۡقَلَمِ ٤ عَلَّمَ ٱلۡإِنسَٰنَ
مَا لَمۡ يَعۡلَمۡ ٥ كَلَّآ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَيَطۡغَىٰٓ ٦ أَن رَّءَاهُ ٱسۡتَغۡنَىٰٓ
٧ إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجۡعَىٰٓ ٨ أَرَءَيۡتَ ٱلَّذِى يَنۡهَىٰ ٩ عَبۡدًا
إِذَا صَلَّىٰٓ ١٠ أَرَءَيۡتَ إِن كَانَ عَلَى ٱلۡهُدَىٰٓ ١١ أَوۡ أَمَرَ بِٱلتَّقۡوَىٰٓ ١٢



(3) Wanda ya gajiyar da kai har ya kusa ya karya bayanka. (4) Kuma mun xaukaka ambatonka, ka wayi gari ana ambatonka a kiran sallah da iqama da sauransu. (5) To tabbas a tare da duk wani tsanani da qunci akwai sauqi da yalwa. (6) Tabbas tabbas a tare da duk wani tsanani da qunci akwai sauqi da yalwa. idan har ka san haka, to kada cutarwar mutanenka a gare ka ta baka tsoro, kuma kada ta kange ka daga kira zuwa ga Allah. (7) Kuma idan ka kammala ayyukan ka, to ka zage dantse cikin bautar Ubangijinka. (8) Ka sanya dukkan kwaxayinka da niyyarka ga Allah shi kaxai.

# Suratut Tin

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Ambaton qimar mutum, da xaukakarsa da addini, da kuma qasqantarsa da wulaqantarsa yayin ta yayi watsi da addinin, don haka Allah ya rantse da wuraren saukar wahayi.

**Tafsir:** (1) Allah ya rantse da vaure, da wurin da yake tsirowa, kuma ya rantse da zaitun da wurin da yake tsirowa a qasar falasxinu, wadda aka aiko Annabi Isa (A.S) a cikinta. (2) Kuma ya rantse da dutsen Saina'u, wurin da ya gana da Annabinsa Musa (A.S). (3) Kuma ya rantse da Makkah, gari mai alfarma, garin da duk wanda ya shige shi yake samun aminci, wanda aka aiko Annabi Muhammad (S.A.W) a cikinsa. (4) Tabbas mun samar da mutum a cikin mafi daidaiton halitta da kyan sura. (5) Sannan muka mayar da shi zuwa ga tsufa a duniya, baya amfanuwa da jikinsa, kamar yadda baya amfanuwa da shi, idan ya savawa yadda Allah ya halicci shi, ya shiga wuta. (6) Sai dai waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi ayyuka nagari, to su waxannan koda sun tsufa, suna da tabbataccen lada marar yankewa, shi ne Aljannah, domin sun tsarkake tarbiyyarsu. (7) To ya kai mutum mene ne yasa kake qaryata ranar sakamako, bayan ka ga dalilai masu yawa a kan ikon Allah?!. (8) Ashe Allah (S.W.T) bai zama mafi hikimar masu hukunci, da mafi adalcinsu ba, da ya sanya ranar alqiyama ta zama ranar bada sakamako ba,?! Yanzu zai yiwu a hankalce Allah ya bar bayinsa kara-zube, ba tare da ya yi hukunci a tsakaninsu ba, ya sakawa mai kyautatawa da kyautatawarsa, mai munanawa da munanawarsa.

# Suratul Alaq

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Bayanin kamalar xan Adam tana tabbata ne da ilimi da wahayi, wanda yake sanya bawa ya rataya da Ubangijinsa, ya ranqwafa masa, da kuma bayanin yadda xan Adam yake tawaya idan ya savawa hakan.

**Tafsir:** (1) Ya kai wannan Manzo ka karanta abin da Ubangijinka yake yi maka wahayi, kana mai buxewa da ambaton sunan Ubangijinka wanda ya halicci dukkan halitta. (2) Ya halicci mutum daga yankin jini daskararre, bayan ya kasance xigon maniyyi. (3) Ya kai wannan Manzo, ka karanta abin da Allah yake maka wahayi, Ubangijinka mafi karamci, wanda babu mai karamcin da ya kai karamcinsa. Shi mai yawan bayarwa ne da yawan kyauta. (4) Wanda ya sanar da yadda za a yi rubutu da zane da alqalami. (5) Ya sanar da mutum abin da bai sani ba. (6) Haqiqa fajirin mutum kamar Abu Jahlin yana wuce iyaka wurin qetare iyakokin Allah. (7) Saboda yana ganin ya wadatu, da abin da yake da shi na matsayi da dukiya. (8) Ya kai wannan mutum, tabbas zuwa ga Ubangijinka za a koma ranar alqiyama, ya sakawa kowa da abin da ya cancance shi. (9) Shin baka ga abin mamaki irin lamarin Abu Jahli ba, wanda yake hana. (10) Bawan mu Muhammad (S.A.W) sallah, yayin da zai yi sallar a gindin Ka'aba. (11) Ba ni labari mana, idan shi wannan da ake hanawa yana kan wata shiriya da basira daga Ubangijinsa?!. (12) Ko kuma ya kasance yana umartar mutane da su ji tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da kuma nisantar abubuwan da ya hana. Yanzu ya dace a hana wanda wannan ne aikinsa?!.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Yardar Allah ita ce mafi qololuwar abin da ake nema. 2 - Muhimmancin karatu da rubutu a musulunci. 3 - Haxarin wadata idan ta sawa mai ita girman kai da nesantar gaskiya. 4 - Hana aiki mai kyau siffa ce daga siffofin kafirai. 5 - Zunubai sun nauyaya bayan Annabi (S.A.W) to ina da sauran halitta kuma?!

أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ١٣ أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ١٤ كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ
لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ١٥ نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ١٦ فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ١٧
سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ١٨ كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ١٩ سجدة

سُورَةُ القَدْرِ — آياتها ٥ — ترتيبها ٩٧

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ فِى لَيْلَةِ ٱلْقَدْرِ ١ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ ٢
لَيْلَةُ ٱلْقَدْرِ خَيْرٌ مِّنْ أَلْفِ شَهْرٍ ٣ تَنَزَّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ فِيهَا
بِإِذْنِ رَبِّهِم مِّن كُلِّ أَمْرٍ ٤ سَلَٰمٌ هِىَ حَتَّىٰ مَطْلَعِ ٱلْفَجْرِ ٥

سُورَةُ البَيِّنَةِ — آياتها ٨ — ترتيبها ٩٨

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لَمْ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ
تَأْتِيَهُمُ ٱلْبَيِّنَةُ ١ رَسُولٌ مِّنَ ٱللَّهِ يَتْلُوا۟ صُحُفًا مُّطَهَّرَةً ٢ فِيهَا كُتُبٌ
قَيِّمَةٌ ٣ وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ
ٱلْبَيِّنَةُ ٤ وَمَآ أُمِرُوٓا۟ إِلَّا لِيَعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ
حُنَفَآءَ وَيُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلْقَيِّمَةِ ٥



(13) Ba ni labari mana idan wannan mai hanawar ya qaryata abin da Manzo ya zo da shi, ya kuma bada baya, shin baya tsoron Allah ne?! (14) Shin mai hana wannan bawa yin sallah, bai san cewa Allah yana ganin abin da yake aikatawa ba, babu abin da yake vuya a gare shi?!. (15) Lamarin ba kamar yadda wannan jahilin yake surantawa ba ne, tabbas idan har bai kame daga cutar da bawanmu, da qaryata shi ba, tabbas sai mun kama shi, mun jawo da makwarkwaxar kanshi da qarfi zuwa wuta . (16) Ma'abocin wannan makwarkwaxa, mai qarya ne a cikin maganganunsa, kuma mai savo ne a cikin ayyukansa. (17) Idan ya so lokacin da zamu kama shi da makwarkwaxar kansa zuwa wuta, ya kirawo abokansa, da waxanda suke zama tare da su a dandali, domin su tseratar da shi daga azaba. (18) Mu kuma zamu kirawo masu tsaron Jahannama, daga cikin Mala'iku, masu kaushi, waxanda basa savawa Allah abin da ya umarce su, kuma suna aikata duk abin da ya umarce su, don haka sai duba ya ga wanne vangare ne cikin biyun nan ya fi qarfi da iko. (19) Lamarin ba kamar yadda wannan azzalumin yake zato ba ne, cewa zai iya shafar ka da wani mummunan abu, don haka kada ka bi umarninsa ko hani, ka yi sujjada ga Allah, ka kusance shi da aikata ayyukan xa'a, don suna kusantarwa zuwa gare shi.

## Suratul Qadri

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Bayanin girman daren lailatul qadri, da falalarta, da abin aka saukar a cikinta.

**Tafsir:** (1) Haqiqa mun saukar da Alqur'ani a dunqule zuwa saman duniya, kamar yadda muka fara saukar da shi ga Manzon Allah (S.A.W) a daren lailatul qadri, a cikin watan Ramadan. (2) Ya kai wannan Annabi, shin kasan kuwa abin da yake cikin wannan dare na alheri da albarka?!. (3) Wannan dare, dare ne mai girman alheri, kuma ya fi wata dubu alheri, ga duk wanda ya raya shi cikin imani da neman lada. (4) Mala'iku suna sauka, kuma Mala'ika Jibrilu ma yana sauka a cikin wannan dare, da izinin Ubangijinsu (S.W.T), suna sauka da duk wani hukunci da Allah ya yanke shi a wannan shekara, na arziki, ko mutuwa, ko haihuwa, ko wanin hakan, daga cikin abubuwan da Allah yake tsarawa. (5) Wannan dare mai albarka, alheri ne gaba xayansa, tun daga farkonsa har zuwa qarshensa, lokacin da alfijir zai vullo.

## Suratul Bayyinah

An Saukar Da Ita A Madinah

**Daga Manufofin Surar:** Ambaton matsayin saqon manzon Allah (S.A.W), da bayyanar saqon, da cikarsa.

**Tafsir:** (1) Waxanda suka kafirta daga cikin Yahudawa da Nasara da mushirikai basu kasance masu barin haxin kan da suka yi ba a kan kafirci, har sai wani dalili bayyananne, da kuma hujja bayyananniya ta je musu. (2) Wannan hujja bayyananniya, da dalili bayyananne shi ne Manzo daga Allah, da ya aiko shi, yana karanta takardu masu tsarki, waxanda babu mai shafar su waxanda aka tsarkake. (3) A cikin waxannan takardu akwai labarai na gaskiya, da hukunce hukunce na adalci, wadda take nusar da mutane zuwa ga abin da yake cikinsa akwai gyaruwarsu da shiriyarsu. (4) Kuma Yahudawan da aka basu Attaura basu yi savani ba, da Nasara waxanda aka basu Injila, har sai bayan da Allah ya aiko Annabinsa gare su, daga cikinsu akwai waxanda suka musulunta, a cikinsu kuma akwai waxanda suka ci gaba da kafircinsu, tare da sun san gaskiyar Annabinsu. (5) Laifi da taurin kan Yahudawa da Nasara yana bayyana, ta fuskar cewa babu wani umarni da aka yi musu a cikin wannan Alqur'ani face da abin da aka umarce su a cikin littafansu, na bautar Allah shi kaxai, da nisantar shirka, da tsayar da sallah, da bada zakka, kuma abin da aka umarce da shi, shi ne addini miqaqqe, wanda babu karkacewa a cikinsa.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Falalar daren lailatul qadri a kan ragowar dararen shekara. 2 - Tsarkake niyya a cikin ibada, yana daga cikin sharuxxan karvar ibadar. 3 - Kafirai su ne mafi sharrin halitta, Muminai kuma su ne mafi alherin halitta. 4 - Haxuwar addinai a tushen aqida, abu ne da yake sa a karvi saqon da Annabawa suka zo da shi.

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ فِي نَارِ جَهَنَّمَ
خَٰلِدِينَ فِيهَآ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ شَرُّ ٱلْبَرِيَّةِ ٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ٧ جَزَآؤُهُمْ
عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدًاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُواْ عَنْهُۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِيَ رَبَّهُۥ ٨

آياتها ٨ — سُورَةُ الزَّلْزَلَةِ — ترتيبها ٩٩

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا زُلْزِلَتِ ٱلْأَرْضُ زِلْزَالَهَا ١ وَأَخْرَجَتِ ٱلْأَرْضُ أَثْقَالَهَا ٢ وَقَالَ
ٱلْإِنسَٰنُ مَا لَهَا ٣ يَوْمَئِذٍ تُحَدِّثُ أَخْبَارَهَا ٤ بِأَنَّ رَبَّكَ أَوْحَىٰ لَهَا
٥ يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْاْ أَعْمَٰلَهُمْ ٦ فَمَن يَعْمَلْ
مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُۥ ٧ وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُۥ ٨

آياتها ١١ — سُورَةُ العَادِيَاتِ — ترتيبها ١٠٠

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْعَٰدِيَٰتِ ضَبْحًا ١ فَٱلْمُورِيَٰتِ قَدْحًا ٢ فَٱلْمُغِيرَٰتِ
صُبْحًا ٣ فَأَثَرْنَ بِهِۦ نَقْعًا ٤ فَوَسَطْنَ بِهِۦ جَمْعًا ٥



**(6) Haqiqa waxanda suka kafirce, daga cikin Yahudawa da Nasara da kuma mushirikai, zasu shiga wutar Jahannama a ranar alqiyama, kuma zasu zauna a cikinta har abada, waxannan su ne mafiya sharrin halitta, domin kafircewarsu ga Allah, da kuma qaryata Manzonsa. (7) Haqiqa waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka aikata ayyuka nagari, waxannan su ne mafiya alherin halitta. (8) Ladansu a wurin Ubangijinsu, shi ne Aljannatai, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu da bishiyoyinsu, zasu zauna a cikinsu har abada. Allah ya yarda da su, yayin da suka yi imani da shi suka yi masa xa'a, su ma sun yarda da shi, saboda abin da ya same su na daga rahamarsa, wannan rahamar da duk wanda ya ji tsoron Ubangijinsa, ya kamanta umarninsa, ya nisanci haninsa, zai same ta.**

# Suratuz Zalzala

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Qwanqwasa rafkanannun zukata, ta hanyar tuna musu hisabi da bin diddigi na sosai.**

## Tafsir:

**(1) Idan aka motsa qasa, motsawa mai tsanani, wanda zai faru ranar tashin alqiyama.**
**(2) Kuma qasa ta fitar da abin da yake cikinta, na mamata da wasun su.**
**(3) Mutum ya ce cikin ruxewa: "Mene ne ya sami qasa take motsawa da jujjuyawa?!**
**(4) A wannan rana mai girma, qasa zata bada labarin duk abin da aka aikata a kanta, na alheri da sharri.**
**(5) Domin Allah ya sanar da ita, kuma ya umarce ta da hakan.**
**(6) A wannan rana mai girma da qasa zata yi girgiza, mutane zasu fito daga filin hisabi daban daban, domin ganin ayyukansu, waxanda suka aikata a duniya.**
**(7) Don haka duk wanda ya yi wani aiki, gwargwadon girman tururuwa 'yar qarama, na alheri da biyayya zai gan shi a gabansa.**
**(8) Duk wanda ya aikata wani aiki, gwargwadon girman tururuwa 'yar qarama na sharri, shi ma zai gan shi a gabansa.**

# Suratul Adiyat

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar: **Bayanin siffofin mutum wajen bada kulawarsa ga abubuwan duniya, domin a tunatar da shi makomarsa, kuma a saka shi ya gyara rayuwarsa.**

## Tafsir:

**(1) Allah ya rantse da dawakai, waxanda suke gudu, har a riqa jin sautin numfashinsu saboda tsananin gudu.**
**(2) Kuma ya rantse da dawakan da suke qyasta wuta da kofatunsu, yayin da kofatun nasu suka tava duwatsu, saboda tsananin yadda suke sauka a kansu.**
**(3) Kuma ya rantse da dawakai, waxanda suke kai hari a kan abokan gaba a lokacin asuba.**
**(4) Suka tada qura saboda gudunsu.**
**(5) Kuma su kutsa tsakanin abokan gaba da mahayansu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: **1 - Tsoron Allah sababi ne na samun yardarsa ga bawa. 2 - Qasa zata bada shaida a kan ayyukan 'yan Adam.**

إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٞ ٦ وَإِنَّهُۥ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٞ ٧ وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ
ٱلۡخَيۡرِ لَشَدِيدٌ ٨ ۞ أَفَلَا يَعۡلَمُ إِذَا بُعۡثِرَ مَا فِي ٱلۡقُبُورِ ٩ (ثلاثة أرباع الحزب ٦٠)
وَحُصِّلَ مَا فِي ٱلصُّدُورِ ١٠ إِنَّ رَبَّهُم بِهِمۡ يَوۡمَئِذٖ لَّخَبِيرُۢ ١١

سُورَةُ القَارِعَةِ — آياتها ١١ — ترتيبها ١٠١

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلۡقَارِعَةُ ١ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٢ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٣ يَوۡمَ
يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلۡفَرَاشِ ٱلۡمَبۡثُوثِ ٤ وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ
كَٱلۡعِهۡنِ ٱلۡمَنفُوشِ ٥ فَأَمَّا مَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ٦ فَهُوَ فِي
عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ٧ وَأَمَّا مَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ٨ فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٞ
٩ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا هِيَهۡ ١٠ نَارٌ حَامِيَةُۢ ١١

سُورَةُ التَّكَاثُرِ — آياتها ٨ — ترتيبها ١٠٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلۡهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ١ حَتَّىٰ زُرۡتُمُ ٱلۡمَقَابِرَ ٢ كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٣ ثُمَّ
كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٤ كَلَّا لَوۡ تَعۡلَمُونَ عِلۡمَ ٱلۡيَقِينِ ٥ لَتَرَوُنَّ ٱلۡجَحِيمَ ٦
ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيۡنَ ٱلۡيَقِينِ ٧ ثُمَّ لَتُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ٨



**(6) Haqiqa mutum mai yawan hana alherin da ubangijinsa yake son ya bayar ne. (7) Kuma shi ma shaida ne a kan hanawarsa ga alheri. Babu ta yadda zai iya musun hakan, domin a fili yake. (8) Kuma saboda tsabar son sa da dukiya, yake rowarta. (9) Shin wannan mutum mai ruxuwa da rayuwar duniya, bai san cewa idan Allah ya tayar da waxanda suke cikin qabari, kuma ya fito da su daga cikin qasa, don yi musu hisabi da bada sakamako, bai san cewa lamarin ba kamar yadda yake zato ba ne?!. (10) Kuma aka bayyana, aka fito da abin da yake cikin zukata na niyya da qudiri da sauransu. (11) Tabbas Ubangijinsu a wannan rana masani ne mai bada labari, babu wani abu na bayinsa da yake vuya a gare shi, kuma zai yi musu sakayya a kan hakan.**

## Suratul Qari'ah

An Saukar Da Ita A Makkah

### Daga Manufofin Surar:

**Qwanqwasa zukata domin su halarto da tashin hankalin ranar alqiyama.**

### Tafsir:

**(1) Lokacin da yake qwanqwasar zukatan mutane, saboda girman tashin hankalin da yake cikinsa.**
**(2) Wannan wane lokaci ne, wanda yake qwanqwasar zukatan mutane saboda girman tashin hankalin da yake cikinsa?!.**
**(3) Ya kai wannan Manzo, me ya sanar da kai wannan lokaci, da yake qwanqwasar zukatan mutane, saboda girman tashin hankalin da yake cikinsa?! Wannan lokacin tabbas shi ne lokacin tashin alqiyama.**
**(4) Ranar da zata qwanqwasa zukatan mutane, zasu kasance kamar qwarin da suka warwatsu a nan da can.**
**(5) Duwatsu zasu zamo kamar audugar da aka kaxa, wajen saurin tafiyarsu da motsinsu. (6) Amma duk wanda ayyukansa nagari suka yi rinjaye a kan ayyukansa munana. (7) To shi yana cikin rayuwa yardadda, wanda zai same ta a cikin Aljannah. (8) Amma duk wanda ayyukansa munana suka yi rinjaye a kan ayyukansa nagari.**
**(9) To wurin zamansa, da matabbatarsa a ranar alqiyama shi ne wutar Jahannama.**
**(10) Ya kai wannan Manzo me ya sanar da kai mece ce wannan wutar?! (11) Wuta ce mai tsananin zafi.**

## Suratut Takasur

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Tunatar da waxanda suka shagalta da duniya mutuwa da hisabi.**

**Tafsir:** **(1) Ya ku mutane, yin alfahari da dukiya da 'ya'ya ya shagaltar da ku daga barin xa'ar Allah.**
**(2) har sai da kuka mutu, kuka shiga qaburburanku. (3) Bai kamata yin alfahari da su ya shagaltar da ku daga barin xa'ar Allah ba, amma da sannu zaku san makomar wannan shagaltar da kuka yi. (4) Sannan da sannu zaku san makomar shagaltar da kuka yi. (5) Tabbas da ace kun sani, sani na haqiqa, cewa za a tashe ku a gaban Allah, kuma ya yi muku sakayya a kan ayyukanku, da baku shagalta da alfahari da dukiya da 'ya'ya ba.**
**(6) Na rantse da Allah zaku ga wuta a ranar alqiyama. (7) Sannan tabbas zaku gan ta, gani na yaqini, babu shakka a cikin hakan. (8) Sannan kuma wallahi Allah zai tambaye ku, game da ni'imomin da ya yi muku, na lafiya da wadata, da sauransu a wannan rana.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Haxarin yin alfahari da fariya da dukiya da 'ya'ya. 2 - Qabari kamar wuri ne na ziyara, domin da gaggawa mutane zasu bar shi zuwa gidan lahira.**
**3 - Ranar alqiyama za a tambayi mutane game da ni'imomin da Allah ya yi musu a duniya. 4 - Mutum an halicce shi akan son dukiya.**

سُورَةُ العَصۡرِ — ترتيبها ١٠٣ — آياتها ٣

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلۡعَصۡرِ ١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ٣

سُورَةُ الهُمَزَةِ — ترتيبها ١٠٤ — آياتها ٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَيۡلٞ لِّكُلِّ هُمَزَةٖ لُّمَزَةٍ ١ ٱلَّذِي جَمَعَ مَالٗا وَعَدَّدَهُۥ ٢
يَحۡسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخۡلَدَهُۥ ٣ كَلَّاۖ لَيُنۢبَذَنَّ فِي ٱلۡحُطَمَةِ ٤
وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحُطَمَةُ ٥ نَارُ ٱللَّهِ ٱلۡمُوقَدَةُ ٦ ٱلَّتِي تَطَّلِعُ
عَلَى ٱلۡأَفۡـِٔدَةِ ٧ إِنَّهَا عَلَيۡهِم مُّؤۡصَدَةٞ ٨ فِي عَمَدٖ مُّمَدَّدَةِۭ ٩

سُورَةُ الفِيلِ — ترتيبها ١٠٥ — آياتها ٥

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصۡحَٰبِ ٱلۡفِيلِ ١ أَلَمۡ يَجۡعَلۡ
كَيۡدَهُمۡ فِي تَضۡلِيلٖ ٢ وَأَرۡسَلَ عَلَيۡهِمۡ طَيۡرًا أَبَابِيلَ ٣
تَرۡمِيهِم بِحِجَارَةٖ مِّن سِجِّيلٖ ٤ فَجَعَلَهُمۡ كَعَصۡفٖ مَّأۡكُولِۭ ٥



# Suratul Asri

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:**
**Bayanin haqiqanin riba da asara a cikin rayuwa, da kuma jan hankali akan muhimmancin lokaci da mutum yake rayuwa a cikinsa.**

**Tafsir:** (1) **Allah ya rantse da lokacin la'asar.**
(2) **Haqiqa kowane mutum yana cikin tawaya da halaka.**
(3) **Sai dai waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma suka aikata ayyuka nagari, kuma suka yi wa juna wasici da gaskiya, da haquri akan gaskiya, to waxanda suka siffantu da waxannan siffofi, sune masu tsira a rayuwarsu ta duniya da lahira.**

# Suratul Humazah

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:**
**Narkon azaba ga masu girman kai, da yi wa addini da ma'abotansa izgili.**

**Tafsir:**
(1) **Wahala da tsananin azaba sun tabbata ga mai yawan gulmar mutane da sukan su.**
(2) **Wanda ba shi da wani tunani sai tara dukiya da lissafa ta, ba shi da wani aiki wanda ba wannan ba.** (3) **Yana zaton dukiyar da ya tara, zata tseratar da shi daga mutuwa, sai ya dauwama a rayuwar duniya.**
(4) **To lamarin ba kamar yadda wannan jahili yake zato ba ne, tabbas sai an wurga shi cikin wutar Jahannama, wadda take valla kuma ta karya duk abin da aka jefa a cikinta, saboda tsananin qarfinta.** (5) **Ya kai wannan Manzo, me ya sanar da kai wannan wutar, wadda take lanqwame duk abin da aka jefa a cikinta?!**
(6) **Haqiqa Wallahi ita wuta ce mai ruruwa.**
(7) **Wadda take keta jikkunan mutane har zuwa zukatansu.**
(8) **Kuma ita dangane da waxanda ake azabtarwa a cikinta a rufe take.**
(9) **Da Wani ginshiqi mai tsawo da aka miqar da shi a kanta, don kada su fito daga cikinta.**

# Suratul Fil

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Bayyana ikon Allah wajen kare xakinsa mai alfarma, domin tunatar da mutane wannan baiwa da aka yi musu.**
**Tafsir:** (1) **Ya kai wannan Manzo, shin baka san yaya Ubangijinka ya aikatawa Abrahata da abokansa ba, ma'abota giwa, lokacin da suka yi nufin rushe xakin Ka'aba?!**
(2) **Haqiqa Allah ya sanya mummunan tanadinsu na rushe xakin Allah cikin tozarta, basu samu abin da suke buri ba, na kawar da mutane daga Ka'aba, basu samu komai ba.**
(3) **Allah ya aiko musu da tsuntsaye, sun zo musu jama'a jama'a.**
(4) **Suna jifansu da duwatsu na tavon da ya dunqule.**
(5) **Sai Allah ya mayar da su, kamar ganyen shuka, wanda dabbobi suka cinye, kuma suka tattake ragowar.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **Asarar duk wanda bai siffantu da imani da ayyuka nagari ba, da yin wasici da gaskiya, da yin wasici da haquri.** 1 - **Haramta qifce da yafuce da gulmar mutane.** 2 - **Kariyar Allah ga xakinsa mai alfarma. Wannan yana cikin amincin da Allah ya hukuntawa wannan xaki.**

سُورَةُ قُرَيْشٍ — آيَاتُهَا ٤ — تَرْتِيبُهَا ١٠٦

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لِإِيلَٰفِ قُرَيۡشٍ ١ إِۦلَٰفِهِمۡ رِحۡلَةَ ٱلشِّتَآءِ وَٱلصَّيۡفِ
٢ فَلۡيَعۡبُدُواْ رَبَّ هَٰذَا ٱلۡبَيۡتِ ٣ ٱلَّذِيٓ أَطۡعَمَهُم
مِّن جُوعٖ وَءَامَنَهُم مِّنۡ خَوۡفِۭ ٤

سُورَةُ المَاعُونِ — آيَاتُهَا ٧ — تَرْتِيبُهَا ١٠٧

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَرَءَيۡتَ ٱلَّذِي يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ ١ فَذَٰلِكَ ٱلَّذِي يَدُعُّ
ٱلۡيَتِيمَ ٢ وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلۡمِسۡكِينِ ٣ فَوَيۡلٞ
لِّلۡمُصَلِّينَ ٤ ٱلَّذِينَ هُمۡ عَن صَلَاتِهِمۡ سَاهُونَ
٥ ٱلَّذِينَ هُمۡ يُرَآءُونَ ٦ وَيَمۡنَعُونَ ٱلۡمَاعُونَ ٧

سُورَةُ الكَوْثَرِ — آيَاتُهَا ٣ — تَرْتِيبُهَا ١٠٨

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِنَّآ أَعۡطَيۡنَٰكَ ٱلۡكَوۡثَرَ ١ فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنۡحَرۡ ٢
إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ ٱلۡأَبۡتَرُ ٣



# Suratu Quraish

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Tunawa quraishawa ni'imar da Allah ya yi musu, da abin da ya wajaba a kansu saboda haka.**

## Tafsir:

**1 Saboda al'adar quraishawa da kuma sabonsu.**
**2 Tafiyar lokacin sanyi zuwa qasar Yemen, da tafiyar lokacin zafi zuwa qasar Sham, a cikin aminci.**
**3 Don haka su bautawa Allah, Ubangijin wannan xakin mai alfarma shi kaxai, wanda ya sauwaqe musu wannan tafiya, kada su haxa shi da wani a wurin bauta masa.**
**4 Wanda ya ciyar da su daga yunwa, kuma ya amintar da su daga tsoro, saboda abin da Allah ya sanya a cikin zukatan larabawa na girmama ka'aba, da girmama waxanda suke zaune a wurin.**

# Suratul Ma'un

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin halayen masu qaryata ranar sakamako da ranar lahira, domin tsoratar da Muminai, da kushe kafirai.**

## Tafsir:

**1 Shin ka san wanda yake qaryata sakamako a ranar alqiyama?**
**2 Shi ne wanda yake ture maraya da qarfi daga buqatarsa ba.**
**3 Kuma baya kwaxaitar da kansa, ko ya kwaxaitar da waninsa a kan ciyar da talaka.**
**4 Halaka da azaba sun tabbata ga masu yin sallah.**
**5 Waxanda suke shagala daga sallarsu, basa damuwa da ita har lokacinta ya wuce.**
**6 Su ne waxanda suke yin riya da sallarsu da ayyukansu, basa tsarkake aiki don Allah.**
**7 Kuma suna hana a taimakawa wasun su, cikin abin da babu cutuwa a cikin taimaka musu.**

# Suratul Kausar

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar: **Baiwar Allah ga Annabinsa (S.A.W) da kuma yanke hanyar masu qiyayya da shi.**

## Tafsir:

**1 Ya kai wannan Manzo, haqiqa mun baka alheri mai yawa, daga cikinsa akwai qoramar Al-kausar wadda take cikin gidan Aljanna.**
**2 Don haka ka godewa Allah akan wannan ni'ima, ta hanyar ka yi masa sallah shi kaxai, kuma ka yi yanka, savanin abin da mushirikai suke aikatawa, na neman kusanci ga gumakansu ta hanyar yi musu yanka.**
**3 Haqiqa mai qin ka, shi ne wanda ya yanke daga dukkan wani alheri, kuma wanda aka manta, ba a ambatonsa sai da mummunan ambato.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mahimmancin tsaro a musulunci. 2 - Riya xaya ce daga cikin cutukan zuciya, kuma tana vata aiki.**
**3 - Godewa ni'ima yana qara ta. 4 - Girman Annabi (S.A.W) a wurin Ubangijinsa, da kiyaye shi, da girmama shi, a duniya da lahira.**

سُورَةُ الكَافِرُونَ — آياتها ٦ — ترتيبها ١٠٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡكَٰفِرُونَ ١ لَآ أَعۡبُدُ مَا تَعۡبُدُونَ ٢
وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ٣ وَلَآ أَنَا۠ عَابِدٞ مَّا عَبَدتُّمۡ ٤
وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ٥ لَكُمۡ دِينُكُمۡ وَلِيَ دِينِ ٦

سُورَةُ النَّصۡرِ — آياتها ٣ — ترتيبها ١١٠

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا جَآءَ نَصۡرُ ٱللَّهِ وَٱلۡفَتۡحُ ١ وَرَأَيۡتَ ٱلنَّاسَ
يَدۡخُلُونَ فِي دِينِ ٱللَّهِ أَفۡوَاجٗا ٢ فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ
وَٱسۡتَغۡفِرۡهُۚ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابَۢا ٣

سُورَةُ المَسَدِ — آياتها ٥ — ترتيبها ١١١

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

تَبَّتۡ يَدَآ أَبِي لَهَبٖ وَتَبَّ ١ مَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ٢
سَيَصۡلَىٰ نَارٗا ذَاتَ لَهَبٖ ٣ وَٱمۡرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلۡحَطَبِ ٤
فِي جِيدِهَا حَبۡلٞ مِّن مَّسَدِۭ ٥



# Suratul Kafiruun

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Tabbatar da tauhidin bautar Allah, da barranta daga shirka, da cikakken bambanci tsakanin musulunci da shirka.

**Tafsir:**

(1) Ya kai wannan Manzo, ka ce yaku masu kafirce wa Allah.

(2) A yanzu ko a nan gaba ba zan tava bautawa abin da kuke bautawa ba na gumaka.

(3) Ku ma ba zaku bautawa abin da nake bautawa ba, shi ne Allah shi kaxai.

(4) Haka ni ma ba zan bautawa abin da kuke bautawa na gumaka ba.

(5) Haka ku ma ba zaku bautawa abin da nake bautawa ba, shi ne Allah shi kaxai.

(6) Kuna da addininku da kuka qirqirar wa kanku, ni ma ina da addini na, wanda Allah ya saukar min da shi.

# Suratun Nasri

An Saukar Da Ita A Madinah

**Daga Manufofin Surar:** Bayanin yadda qarshen lamarin musulunci zai kasance, na samun nasara, da buxe garin Makkah, da bayanin abin da aka shar'anta idan hakan ya faru, kamar yadda surar take nuna kusancin ajalin Manzon Allah (S.A.W).

**Tafsir:** (1) Idan taimakon Allah ya zo wa addininka - Ya kai wannan Manzo - da xaukakawar Allah ga addinin. kuma buxe Makkah ya tabbata. (2) Ka ga mutane suna shiga addinin musulunci, jama'a bayan jama'a.
(3) To ka sani cewa wannan alama ce ta kusantowar qarshen aikin da aka aiko ka da shi, don haka ka tsarkake Ubangijinka, da yi masa godiya, godiya gare shi a kan ni'imar samun nasara, da buxe garin Makkah, kuma ka nemi gafararsa. Haqiqa shi mai yawan karvar tuba ne, yana karvar tuban bayinsa, kuma yana gafarta musu.

# Suratul Masad

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** Nasaba ko matsayi basa amfani matuqar mutum ya kafirce wa Allah.

**Tafsir:**

(1) Hannayen baffan Annabi (S.A.W) Abu Lahab xan Abdulmuxxalib sun tave, saboda tavewar aikinsa, domin ya kasance yana cutar da Annabi (S.A.W), don haka aikinsa ya lalace.

(2) Wane abu dukiyarsa da 'ya'yansa suka amfana masa?, basu kare masa azaba ba, kuma ba su jawo masa rahama ba. (3) Ranar alqiyama zai shiga cikin wuta, mai ci bal bal, kuma yasha fama da zafinta.

(4) Haka ma matarsa Ummu Jamil zata shiga wuta, wadda ta kasance tana cutar da Annabi (S.A.W), ta hanyar sanya qaya a hanyarsa.

(5) A jikin wuyanta akwai igiya mai qwari, wadda da ita za'a ja ta zuwa wutar.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Rabuwa da kafirai.
2 - Fuskantar ni'ima da godiya. 3 - Suratul Masad xaya ce daga cikin dalilai masu tabbatar da Annabtar Manzon Allah (S.A.W), domin ta yanke hukuncin cewa Abu Lahab zai mutu kafiri, kuma bayan haka da shekara goma ya mutu akan kafircin. 4 - Ingancin auratayyar kafirai.

سُورَةُ الإِخْلَاصِ — ترتيبها ١١٢ — آياتها ٤

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلْ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ٢ لَمْ يَلِدْ وَلَمْ يُولَدْ ٣
وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدٌۢ ٤

سُورَةُ الفَلَقِ — ترتيبها ١١٣ — آياتها ٥

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلْفَلَقِ ١ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ٢ وَمِن شَرِّ
غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ٣ وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِى ٱلْعُقَدِ ٤
وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ٥

سُورَةُ النَّاسِ — ترتيبها ١١٤ — آياتها ٦

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ١ مَلِكِ ٱلنَّاسِ ٢ إِلَٰهِ
ٱلنَّاسِ ٣ مِن شَرِّ ٱلْوَسْوَاسِ ٱلْخَنَّاسِ ٤ ٱلَّذِى
يُوَسْوِسُ فِى صُدُورِ ٱلنَّاسِ ٥
مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ ٦



# Suratul Ikhlas

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Tabbatar da kaxaitakar Allah da kamala da bauta, da tsarkake shi ga dukkan tawaya.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Manzo ka ce, Shi ne Allah, wanda ya kaxaita da bauta, babu wani abin bautawa da gaskiya wanda ba shi ba.**

**(2) Shi ne shugaban da shugabanci ya tuqe gare shi, a cikin siffofin kamala, da kyau. Kuma shi ne wanda dukkan halittu nufa da buqata zuwa gare shi.**

**(3) Wanda bai haifi kowa ba, kuma babu wanda ya haife shi, don haka Allah (S.W.T) ba shi da xa, ba shi da uba.**

**(4) Kuma babu wanda ya yi kama da shi a cikin halittarsa.**

# Suratul Falaq

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Neman tsari, da yin riqo da Allah, daga dukkan sharri bayyananne.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Manzo, ka ce, ina fakewa da Ubangijin asuba, kuma ina neman tsarewar sa.**

**(2) Daga sharrin dukkan abin da yake cutarwa daga halittu.**

**(3) Kuma ina neman tsari da Allah daga dukkan sharrin da yake bayyana cikin dare, na daga dabbobi ko varayi.**

**(4) Kuma ina neman tsari da shi daga sharrin mata masu sihiri, waxanda suke yin tofi a cikin qulle -qulle.**

**(5) Kuma ina neman tsari da shi daga sharrin mai hassada, yayin da ya yi aiki da abin da hassada ta sa shi.**

# Suratun Nasi

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Neman tsari, da yin riqo da Allah daga sharrin Shaixan da wasiwasinsa, da kuma voyayyun sharri.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Manzo, ka ce ina neman tsari da Ubangijin mutane, kuma ina fakewa da shi.**

**(2) Mamallakin mutane, wanda yake yadda ya ga dama da su, basu da wani mamallaki wanda ba shi ba.**

**(3) Abin bautawarsu da gaskiya, babu wani abin bauta da gaskiya wanda ba shi ba.**

**(4) Daga sharrin Shaixan, wanda yake jefa wasuwasinsa ga mutum, yayin da ya rafkana ga ambaton Allah, yake baya da shi idan ya ambace shi.**

**(5) Shi ne wanda yake jefa wasuwasinsa a cikin zukatan mutane.**

**(6) Kuma yana kasancewa daga cikin mutane, kamar yadda yake kasancewa daga cikin aljanu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**5 - Tabbatar da siffofin kamala ga Allah, da kore masa siffofin tawaya.**

**6 - Tabbatar da sihiri, da hanyar da ake maganinsa.**

**7 - Ana magance wasuwasi da ambaton Allah, da neman tsari daga Shaixan.**